AYI DAI MU GANI

3

NA

HAJIYA HAFSAT C. SODANGI
(Mrs. Abdullahi Yunus Dabai)

1

GODIYA

Godiya ga Allah ta ke, Madaukaki,
Makadaici, mai kowa mai komai Mahalaccin
sammai bakwai da kassai bakwai da abin da ke
tsakanin su.
Tsira da amincin Allah su tabbata ga
cikamakin Annabawa, shugaban Manzanni,
Annabin Karshe Muhammadu (S.A.W) da
Alayensa da sahabbansa da wadanda suka bi ma
tafarkinsa na gaskiya har zuwa ranar tashin
kiyama, amin summa amin.
Bayan haka godiya mai dinbin yawa ga
makaranta litattafaina, na nesa da na kusa na
gode kwarai da zumuncin da ku ke nuna min, na

gode.

28/7/2010

3

TUKUICI

Tukuicin littafin na jama'ar da suka halacci bikin Aisha ne da angonta Isma'il Abubakar.
Na gode da zumuncin da ku ka nuna min, da fatan kowa ya koma gidanshi lafiya, amin.

JINJINA

Jinjinar taku ce.
Daukacin masoya da ke cikin garuruwan Zindar Maradi, Warah, illelah da Kamba na gode kwarai da kuiawarku, ina kuma saduwa da sakonninku, na gode.

4

FADAKARWA

AYI DAI MU GANI...littafi ne da aka rubuta shi don fadakarwa da nishadantarwa kawai wanda duk wani abu ya yi kama da abin da ya same shi, to ba da shi ake ba, dace ne kawai ana kuma neman gafarar shi in har hakan ya sosa mishi rai, na gode.

H. C. Sodangi

Hakkin Mallaka

Hakkin mallakar littafin AYI DAI MU GANI.

Na marubuciyar shi ne,

HAJIYA HAFSAT CHINDO SODANGI

Don Allah a kula.

GAISUWAR SADA ZUMUNCI

Halima Kurabau (Kishiyar Kwarai)

Hafsat Muhammad Aminu

Hajiya Indo Zailani Katsina

Hadiza U. Audi (Maman Imam)

Aishatu Isa B. Wairi Buba Shango, bayan

Fadama two Gombe,

Sanda Zainu

7

GAISUWA GARE KU

Mallam Murtala mai littafin Hausa cikin asibitin

gawonnama FSSS kusa da masu sayar da

mashina cikin garin Sokoto.

8

INA SANE DA KU

Marliya Y. Buhari.

Haj. Jummai Aliyu (Mrs Ado Basiru Kaure),

magama kwatas.

Basira Muhammad Isyaku Babura

Haj. Aisha Lamido S. Tuchu Sokoto

Rahane Sani Dankani Katsina

Binta Idris (Ummi) Malunfashi, Katsina state

Rashida Almu Sheshe

Fatima Dangaskiya Sokoto

Farida S. Kangi

Fatima Ibrahim Riciya

Zakiyya Abdullahi Katsina

na gode.

9

GORO GARE KU

Sameera Gambo Dage-dage

Rabi'atu Hashim Mera Argungun, Kebbi State

Sadiya Musa Gani Katsina

Saratu Usman Inuwa, Z0o Road, Kano

Zulaihatu Ahmad

Na gode da kulawarku.

10

Littattafan SODANGIE

Uwar Miji

Naga Ta Kaina

Rabon Kwado.

Cikar AIkawari

Yiwa Wani...

Abu Naka...

Tabbataccen Al'amari

Nufin Allah

Kifi Na Ganinka...

Gani Gare ka...

Mata Masu Duniya

Me Zamu Ce Da Maza?

Biyan Bukatar Rai

Hattara

Daga Kin Gaskiya...

Da Kamar Wuya...

Shamaki

Mata Da Kicin Dinsu

Duk Daya

Mai Uwa...

Wacece Ni?

Ayi Dai Mu Gani..

Garin Banza..

Waiyo Duniya!

11

A YI DA MU GANI...3

Wai daga kawai na dan kurma ihu
don in samu in dan ji dadi in ji
saukin gululun bakin cikin da ya tokare ni, ya
tsaya a tsakanin makogwarona yake nema ya
tarwatsa min shi da radadin ciwo saboda
tsananin damuwa da 6akin ran da nake ciki
na wulakanti, cin zarafi da rashin tausayin da
Wada mai shayi ya gwada min.
Wada mai shayi ka cuce ni, Wada mai
shayi ban yafe maka ba, wayyo Allahna,
wayyo Wada, ai ko da na tafi na bar dana
kasan ina sonshi tunda dai jikina ya tsaga ya
fito zuwa na yi kawai don in sauke wani
nauyi dake kaina, in dawo gare shi ba wai ina

nufin na tafi kenan ba."
Abin da ke ta fitowa daga cikin zuciyata
ke nan babu juyin da ban yi da ita ba ta daina
jero min irin wadannan maganganun don
bana son jin su ta ki yarda ta bari.
Na yi wani juyi na kautar da fuskata daga
fuskantar bango na juyo ta wani gefen ko zan
samu saukin maganganun nata, sai kawai na

ji ta ta canza salo, kalmomin da na ji Inna
tana ambata lokacin haihuwar yaron take jero
min.
"Yau ga yaro da kyau ga shi gabjejc gashi
tubarkallah kamar ubanshi, kai wannan da da
kama da uba yake dan juyo da fuskarki tana
ki ganshi kin taba haihuwa mai dadin wannan
kuwa?
Zumbur na yi na tashi na yi zaune akan
katifar saboda in yi maganin mita da kananan
maganganun da take damuna da su tunda dai
ita din na lura bata da wani aikin da ya wuce
magana da shiga cikin abinda ba a sanya ta
ba.

Mikewan nawa ke da wuya, sai kawai idanuwana suka kai kan nonuwana da suke tsaitsaye suka cika suka yi tantsam-tantsan sai faman zuba suke ta yi, kafin kallon da nayi musu din na mance cewar har da su cikin al'amuran da suka dame ni. Na dan juya kadan na kalli wurin da da nake kwance sharkaf yake a jike alamar dai sun dade da fara zuban kenan. Na sake dawo da kallona a gare su cikin ajiyar zuciya na ce ha.....

13

Cikin abubuwan da suka hadu suka haifar min da matsanancin zazzabin da nake fama dashi. Ina zaune ni kadai a daki sai faman kaduwa nake yi a duk lokacin da na kalli kirjin nan nawa kuma hankalina sai ya kara tashi, saboda tuna maganar da nake yi na cewar nono kan cika ne ya yi ta zuba a lokacin da jajarin shi ya ke neman shi, ko kuma ya farka daga bacci, to ni ko ina nawa jaririn ya ke? Oho.
Da damuwa ta yi mun yawa sai na kasa Jurewa, kaina wani irin juyi yake yi mun ga

kirjina da bayana kamar za su hade wuri, makogwarona kuwa ya fi komai gana mun azaba don kuwa ya dade yana kokarin ballewa, tunani mai zurfi ya zo min sai naga watakila don na hana kaina yin kuka ne yasa wadannan abubuwan duka suke damuna. Ina yin wannan tunanin sai kawai nayi maza na goge bakina da iyakacin karfina na kama ihu yace in har kukan zan yi to ya kamata ne in yi har ya ishe ni don in samu saukin damuwata. Ni daya kawai na kurma ihun, sai ga Inna ta zo bakinnkofar taja ta tsaya tana ta faman

waige-waige. Ni kuwa sai na kawar da kaina can gefe nayi kamar ban ga tsayuwar tata ba, na ci gaba da ihuna da iyakacin karfina, cikin zuciyata dai fadi nake yi a yanzu ne zaku gane ina da damuwa da ku ka jini ina ihu amma da da na yi shiru ba ku kula ni bä kun barni ina fama da bakin ciki ni kadai tamfar ba mutum aka sace min ba.
Sanin da na yi Inna tana nan wurin a tsaye kuma har lokacin ba ta karaso ta kama bani

hakuri ba, sai na ce to bari in hada ihun nawa da birgima don ta kara sanin ina cikin wani hali in ta tashi rarrashin nawa tasan irin wanda zata yi, tasan irin dadadan kalaman da zata shirya ta gaya min masu dadi da kwantar da hankali, tunda dai na san tana sona ni ce 'yarlelenta, na kuma san tasan nima ina son wannan dan jariri da aka sace min aka raba ni. da shi aka gwada mana rashin tausayi da rashin Imani wajen yanke mana mu'amalla, mu'amallah mai dadi da aka sani na tsakanin da da mahaifiya, dan ma kuma a ce dan jariri na san dole Inna ta tausaya min matsanancin tausayi..

15

Ina nan a kwance cikin lunshewar ido da gurnanin kuka ina kuma sauraron karasowar tagare ni ta soma bani hakurin, sai ka wai na ji an sakan min sanda a baya tim, da iyakacin karfi sai da na ji bayana ya sandare. A gigice kuma na kurma ihun da yafi kowanne kara don na yanzu kam bana bacin rai ba ne na wahala ne, kan kace meye wannan tuni jikina ya ji jiki, ya kuma yabawa aya zakinta, don

kuwa ta ko ina dukan sai sauka mishi yake yi, watakila ma ba mutum daya ba ne don ta ko'ina jin saukar sandunan nake yi da kyar na yi jarumtakar da na matso da natsuwata gare ni na iya bude idanuwana don in shaida su wanene masu gana min wannan azabar? Abin mamaki Inna na gani ita kad ai ce take ta faman jibgata ta duka kuma wai har da na shaida ta na kama ambaton sunanta bata daina ba, ashe wai waige-waigen nan da naga tana tayi ashe abin dukana take ta nema, na ce wayyo Allah, Inna waiyo za ki kashe ni. Tana dukan nawa tana fadin.

"Gara dai in kashe kin abin da na ke son yi ke nan ko ma samu zaman lafiya da

kwanciyar hankali a gidan nan, in muka huta da irin abin bakin cikin da ki ke jawo mana." Yaya Buhari ya shigo cikin dakin yana fadin.

"Haba Inna, haba Inna, tana jego kina mata irin wannan dukan ai sai ki ji mata ciwo,"

Yasa hannu ya karbe sandar dukan daga hannunta.

"Hakuri kawai ai za ayi ta yi da ita Inna, in aka ce za'a biye mata ai sai ayi abin da za'a zo ana cewa da an sani ba'ayi ba, sannan ita din tausaya mata ya kamata ayi ba a yi fushi da ita irin wannan fushin ba."

A fusace ta ce mishi.

"Ba zan tausaya ba, na kuma cewa ba zan tausaya mata ba, ita tasan tausayi ne? Wa ka taba gani ta tausayawa? Mai tausayi zai iya yin abin da wannan ta yi? Don me zan zauna ina tausayinta tsofai-tsofai da ita alhalin ita din ba zata tausayawa dan jaririn da bai san komai ba? Haba, me za'ayi da mai irin wannan halin? Me za'ayi da Rahina da al'ama rinta?Yanzu wannan abin da ta jawo mana

dame ya yi kama? wannan wane irin abu ne a dauki jariri mai kwana uku a tafi dashi?"

Tana fadin hakan ta fashe da kuka, tana fadin "Kuma duk laifinta ne ita ta jawo ban taba ganin jairar matar da ta haihu ta wulakanta haihuwar ba irin ta, mutane nawa

suke nemanta ba su samu ba? Ni sai yaushe zan fita a cikin fitinar wannan yarinyar? Kullum a cikin fitinarta nake nan gidan babu abin da bata jawo mana ba har cikin abin nan taje ta dauko amma na ce sam ta ki karasa maganar alamar har yanzu bata mata dadi ta ci gaba da kukan da take yi har tana face majina.

"Hakuri fa za ki yi Inna, wannan tone-tonen duk ba naki ba ne, don in wani ya ji kuma ya kama ya rike ya fadi a wani wuri a wani lokaci sai ki ga zuciya bata so ba."

Tana kukan ta ce, su je su fada su je su yi ta fadin abin da suka ga dama, wane irin magana ne bata jawo min ba? Yaya zan yi da rayuwata? Ni na hakura, na hakura da ita, na kuma rigaya na fidda ita a zuciyata."

"Uh'un Inna, mu bar maganar nan a haka kiyi hakuri kar ki tsananta fushinki a kanta don hakan ba zai zamo alheri a gare ta ba."

Tuni na kwanta a kasa na yi lamo na daina kukan da nake yi, sai zazzare ido da

rarraba su saboda tsananin tsoratar da nayi da ganin mahaifiyata tana kuka a dalilin bakin cikin abin da nake yi ko na yi mata yau na gamu da gamuna yau ga Inna tana kuka a gabana saboda gajiya da abubuwan da nake jawo mata kuma da bakinta take fadin bakin cikina ya ishe ta. Na sake fadin "Wayyo Allahna, wayyo na gamu da gamona, tawa kuma ta same ni.

"Hakuri fa za ku yi Ina ku bar wannan koke-koken da kuke yi don ba alheri ba ne. Ta ce to in ban yi kuka ba me zan yi? Randa ka haifi dan da yafi karfinkaa bai jin maganarka bai ganin girmanka ai taka ta same ka."

Cikina ya yi maza ya ba da sautin kululululu a dalilin jin da na yi Inna tana cewa, wai na fi karfinta a haka ake fin karfin iyayen ashe? Na sake zaro idanuwa, ina kalle-kallén cikin

kokarin da nake yi na tuna yanda fin karfin iyayen yake, Inna ta ci gaba da kukan da take yi cikin tsananin nadama Yaya Buhari ya sake kallonta ya ce mata.

"Hakuri fa za ku yi Inna, ku yi hakuri." Ta sake cewa, "To yaya zan yi? In ban yi hakurin ba? Zan yi aman zuciyata ne? Ko kuwa wata magana zan gaya mata in ji sanyi ko in ji na hce? Ai babu daya don haka hakuri ai ya zame min dole in yi shi." Kalaman da take yi din ba su hana ta kukan da take yi ba shi kuwa yana ganin zata kauce daga kalaman yarda da hakuri ta fadi wata magana ta Bacin rai sai ya shiga cewa. "Uh'uh Inna, hakurin dai da ki ka ce shi ya kamata kiyi." Yanzu shi kenan ba zan sake ganin wannan yaron ba'? Bai bata amsa ba va dai lallabata suka shiga cikin dakinta.
Suka barni nan wurin a kwance lamo bana ko motsi tsawon daren rannan ban yi gyangyadi ba, balle in samu in runtsa, ba tunani ne kawai a cikin zuciyata na abin da ya faru tsakanina da mahaifiyata ban taba sanin hakan zai iya faruwa ba, ban taba ganin

fushinta a kaina ba balle har aje ga bacin rai mai yawa, ban taba tunanin wani abu gamne

da ita na damuwa, nan take sai na samu zuciyata da tunanin ashe dai dama akwai mas'ala tsakanina da ita, ashe dai dama hakuri kawai take yi dani, ashe dai dama al'amura suna yi mata ciwo dannewa kawai take yi.

Washe gari wunin ranar tun safe har yamma ban ji motsin fitowar Inna tsakar gida ba, na dai ji zuwan Baba Rahina ita ce mai kai kawo a tsakar gidan, haka nan tunda na ji shigowar Yaya Buhari bayan sallar azahar ban ji fitarshi ba, ba kuma lokacin zuwan shi ke nan ba. To ko dai Innan bata da lafiya ne? Gabana ya yi mummunan faduwa saboda zuwan da wannan tunánin ya yi cikin zuciyata, na yi maza na kawar da wannan tunanin ta hanyar cewa kila dai hirarsu kawai suke yi, ba wata damuwa ke gare ta ba, tunda nasan ya kan zo ya zauna tare da ita su tattauna al'amura masu yawa.

Duk da kawar da tunanin rashin lafiyar Inna da na yi ban samu kwanciyar hankalin

da nake bukata ba, saboda harbawan da

gabana yake yi na kasa samun kwanciyar hankalin da nake bukatar samu, gabana sai faduwa yake yi ni kuwa da táwa ta same ni in dai aka ce a wannan lokacin Inna ta rasa lafiyarta.

Hawaye, suka kama zuba daga idanuwana shar! shar!! Shar!!! loakcin da na tuna yanda al'amurana suke tafiya babu wani abin da na taba sanyawa a gabana na yi nasara a kanshi babu wani abin da na taba neman na same shi yanda nake sonshi ko zai zo min to yakan z0 munne a karkace bata yanda na neme shi ba. Duk wani abin da na nema to kuma na kan same shi ne a hanyar da ba zan ji dadin shi ba, haka nan ban taba son wani abu ba sai na rasa shi a daidai lokacin da nake matukar bukatarshi fiye da kowane lokaci, tausayin kaina ya kama ni a daidai lokacin da na tuna a yau na rasa soyayya da tausayawa irin ta uwa mahaifiya ga yarta uwar ma kuma wai irin Inna mai yiwa da tatalin abin da yake so ta kuma taya shi kin abin da ba ya so, ba tare

da ta damu da yin bincke ko neman sanin

dalilinshi na son ko kin ba.
Gani a yanzu cikin tsananin damuwa da kunci a daidai lokacin da nake bukatar soyayya da tausayawa irin ta da da mahaifi, na rasata wai Inna ce ta dauko sand atana jibgata da duka da ita, a daidai loka cin da nake cikin damuwa da kunci a yanzu da nake matukar bukatar ta tausaya min ta rarrashe ni ta hanyar zaunar dani ta gaya min maganganu masu dadi da kalmomi masu nutsar da zuciya, in dan samu in ji sanyi in dan samu in ji saukin damuwar da nake ciki bayan kuma bani da lafiya na kuma san tafi kowa sanin ciwona.
Kullum a sanina Inna a sona take tana kuma tattalina tana g udun bacin raina tana kokarin ganin farin cikina, a duk lokacin da nake cikin damuwa to tana cikinta, to gashi na kureta, ta zama bata sona, bata tausáyina, bata tattalin ganin farin cikina, ni kuwa a rayuwata wanne irin hali ne dani? Mene ne kuskure na? Menene dalilin da na ke gamuwa da irin wadannan abubuwa? Tambayoyin da

ban iya baiwa kaina amsar wadannan tambayoyin ba, illa iyaka dai na yankewa suka rinka zuwa min ke nan cikin zuciyata, kaina hukuncin da zaman zullumin da nake ciki, to me zai hana ni, zawa wurin Inna kawai in dubu ta in ga halin da take ciki, in ga lafiyarta don in samu nutsuwar zuciyata. Kokarin da na yi na in tashi zaune in da hali ma in mike gaba daya in nufi wurin nata shi ne ya fahimtar dani cewar yin hakan ba abu mai sauki ba ne a wurina saboda jina nayi tamfar an kafe ni a kasan saboda tsananin nauyin dake jikin nawa, gaba daya na kasa motsa gabobina bałle in iya sarrafa su a dalilin ciwon da jikina ke yi. Wayyo Allah, wayyo Allahna na fadi kalmar cikin tsananin wahala.

Na yi shiru ina tunanin menene ya same ni haka? Zuwa can dai sai na gane tsami ne ya hada da tsami ga dai tsamin jikin nakudar da aka yi aka yi haihuwar da ba a samu kwanciyar hankali ba a cikin ta balle a sa ran samun kulawar da ta ce dace ko wankan arziki ban samu na yi ba, balle a samu zarafin

yin wasu gashe-gashen da suka dace, to ga kuma tsamin duka abin da rabon da ayi min shi an samu shekaru masu yawa, na manta yanda wahalarshi take ko a wancan lokacin kuma ni mai tsoron duka ce in na tsokano abin da za ayi min shi to jikina ya rinka 6ari kenan bana samun natsúwa sai na ji an ce an yafe min ko kuma an yi an gama.

Ganin da na yi motsa jikin nawa bai zame min al'amari mai sauki ba sai na koma na yi kwanciyata lamo kan yar katifata cikin. zuciyata dai fadi nake yi, kar dai ace garin fushin zuciya Inna targada min gabobin nar nawa ta yi? Ina wa.man tunanin cikin raina yayin da idanuwana kuwa nake rarraba su tsakar gida, fata nake wai inga wucewar wani wanda zan kira in tambaye shi labarin Inna don na ji shirun nata ya yi min yawa. Ina cikin haka sai na hango wucewar Baba Rahina da sauri na kwala mata kira har sau biyu bata amsa ba ga dukkan alamu kuma ta Ji amsawa ne kawai ba zata yi ba na yamutsa na taba baki cikin zuciyata kuma na cewa kaina ni Rahina ta ya ta same ni.

Zuwa can na sake ganin gilmawar ta na yi maza na sake kwala mata wani kiran "Baba, Baba." Ta zo ta tsaya.daga bakin kofar dakin fuskarta a yatsine ta ce min "Menene ki ke ta faman kwala min kira kamar wata tsohuwar makauniya? Na dan dago ido na kallc ta da nufin yi mata magana, mazuran da na gani a tare da ita ya Kara fadar min da gaba, gaba daya na mance da dalilin kiran da nayi mata na soma kame-kamen abin da zan gaya mata ina fadin "uh'uh, taja wani mummunan tsaki kafin ta ce "dama tsaida ni kawai kika yi nufin yi? Da sauri na ce mata "A'a Baba kiyi hakuri wai so nake ki taimake ni ki daga ni, ta karaso dakin tana cewa "Uhh, lalle aiki ne ya same ni ja kuwa, in daga uwarki kema in daga ki? Cikina ya bada sauti mai karti na kulululu! Har itama sai da ta ji kukan nashi daga Inna? A firgice cikin rashin sani nayi mata tambayar, ta ce ba za'a daga taba bakin ciki wasa ne? ko da yake dai bata da wata matausaya sakamakon abin da ta shuka né

take girba, a kanki menene bata yiwa mutane ba? Ta daure miki gindi kika ci karenki babu

babbaka, babu wanda ya isa ya ce kin yi ba daidai ba, sai tayi damarar yin tashin hankali dashi kici mutuncin na gaba da ke kiyi mishi rashin kunya da rashin mutunci babu yanda zai yi dake saboda uwarki ta tsaya miki, babu wanda ya isa ya hukunta ki kan al'amuranki saboda ana tsoron masifarta, to ai ke kya hukuntata ko? Kinga a in da bata koyi tarbiya ta iya ba yanzu ke kya koya mata yanda ake yi, nan gaba in ta kara haihuwa sai tasan yanda ta yi ta yi tarbiyar yaron don kar ya zamo mata abin da ki ka zamo mata, don wannan kifi kafin da take yi dai yau kam da kyar in ba hawan jini ba ne ya kama.... "Da sauri na katse ta kai Baba, haba Baba, na Soma kuka.

Ta sake yamutsa fuska ta zobara baki kafin ta sake kallona, cikin mazurai ta ce "Ke tafi can ni kikewa tsawa? Hawan jini ba zai kama ta ba wa tafi gata? Mu da muke fama dashi tare da sauran Jama'a mutanen kirki aka.

ce miki ba ayi? Balle Maude, mu fa a kanki sai da ta zagi zuriyarmu kaf gaba daya ta yi mana jam'i ta sheganta mu ta kira mu masu

gadon cikin shege, don kawai an fadi gaskiya a kanki, ko a gidan uwar wa ta ji mun taba yin shi oho? Ta sake jan kwafa mai tsananin karfi ta ce Uhum, ai ni ko wannan dawainiyar da nake ta yi da ita nake ta faman kwashe mata aman da nake yi darajar abu biyu ta ci, zumuncin da ke tsakanina da wana ko da dai ba barina tayi na ji dadin shi ba, sai ko darajar wannan yaron Buhari, in ban da haka ko kallon kofar gidan nan ba zan yi ba, da sai dai in yi wucewata ba zan zo ba, balle in taya ku ganin abin takaicin ku randa ki ka kwabo wata tsiyar mai girma kya zama sanadinta, shi mutum ai dama shi ne bai sani ba amma mafi girman tsiyar da yake aikatawa ai kan shi take dawowa."

Na zubawa Baba Rahina ido, ina kallonta cikin zuciyata magana nake yi da ita, sai dai babu halin in furta mata darajar tana kanwar mahaifina fadi nake yi yanda Inna ke cin

arzikin mijinta da danta a wurinki haka nima
kike cin arzikin dan uwanki a wurina sanin
da na yi ke din kanwa ce a wurinshi yasa ki
ke gaya wa uwata irin wadannan munanan

maganganun a gabana ina jin ki ina kuma
kallonki, amma babu yanda zan yi dake in
ban da darajar tashi du kema kin sha mamaki.
Ban jira ta daga min ba na yi yunkurin da
na mike na yi waje na barta a dakin kai tsaye
dakin Inna na nufa.
Yaya Buhari yana tare da ita tana kwance
sai numfashi sama-sama take yi kuma da kyar
da kyar, kar dai ace hawan jinin ne ya kamaa
ta? Ai kuwa dai kam da na gamu da gamona,
kuma da tawa ta same ni, ace dai saboda ni ne
a dalilina mahaifiyata ta samu lalura da ina
zan shiga in tsoma rayuwata in ji dadi?'
Kasa karasawa jikin gadon na yi, na
durkusa daga can gefe saboda kukan da na
tarar Innan tana yi, jikina ya dauki rawa
idanuwana suka kama zubar da hawaye, a
lokacin da zuciyata ta tabbatar min da cewar
lalle ne na yiwa mahaifiyata al'amari mai

girman da ya tsananta a wurinta yanzu ina
Zan ga yaron nan? Yanzu ina, zan shiga in
nemo shi? ai ni ina sonshi ina kuma
tausayinshi in ban da al'anarin Wada ai ya ce
ni uwarshi ce ai da sai ya bar min yaron in

rike mishi shi, ko da yake dai ba laifinshi ba
ne ga wacce taja nan ita ta wulakanta shi,
saboda bata san darajar mutum ba, saboda
taga tana haihuwarsu ba tare da ta wahala ba,
gani take tamfar haihuwar abin banza ne, bata
san akwai dubban mutanen da suke nema
basu samu ba, waiyo kaina kama mun nan,
daure min nan ta na fadin maganar tare da
muna inda take so aka ma mata akan nata ko
kuma a daure matan, na yi maza na nufi inda
take kwancen da nufin bayar da gudumawata
wajen rike mata kan ko daure mata shi, sai
kawai na ji ta kama fadin matsa daga nan
kauce ki bani wuri bana son sake ganin
inuwarki kusa dani."
Da sauri naja da baya na tsaya yayin da
Yaya Buhari ya kama bata hakuri.
"Ki yi hakuri Inna, itama Rahina ai ba

dadin hakan take ji ba, Baba Rahina ta yi maza ta ce "A'a kul bana son daurewa kar ya gindi mutum ya yi sanadin faruwar al'amari da kanshi sannan kazo kana cewa bata ji dadi ba? Kar in sake jin irin wannan maganar tana fitowa daga bakinka, fita ni ki bamu wuri ga

ruwa can na kwashe miki a kwatarniya na kuma ajiye miki ganyen runhu in kin ga dama kije kiyi wanka mai kyau, in ba ki gani ba ki yi abin da ki ga ya yi miki, in danta ta kama ki ke ki ka jiwo, kuma duk haihuwar da ki ke yi ba ki san wai ki dan bugi jikinki da runhu ki Ji dadi ba."

Na kama hanyar bandakin ina tunanin sauran haihuwar da take magana akai ita ce ta yi min zaman jego, tun ma kan haihuwar tazo nake dauko ta akan idonta ake komai ita din ce kuma mai gaya min cewar cin abinci shi ne jego ba sai na je ina ta wahalar kwarawa jikina ruwan zafi ba, in je kawai in tayar wa jikina da hawan jini, ai su iyayensu a da wahala kawai suke yi ta basu da sunan biki.

Na zauna kan kujera na dauki runhun da
na tarar watse a kasa na gyara su yanda zan ji
dadin rike su a hannuna na tsoma su cikin
ruwan sanyi na wanke su sannan na girgijé
ganyen sosai na tsabtace shi kafin na tsoma
shi cikin ruwan zafin da na soma zubawa a
jikina cikin zuciyata kuwa fadi nake yi, nima

a wannan haihuwar nima nasan wankan
runhun ne ya kamacc ni.
Ina zaune a dakına ina shata mai bayan na
gama dukan jikina da runhu cikin zuciyata
kuma fadi nake yi, in dai har wankan runhu
da tafasasshen ruwa yana da wata illa to
kuma dai yana da wani amfanin don gani ni a
yanzu ji na nake garau dani tamfar ba ni ce
dazu tsamin jikina ya hana ni in iya sarrafa
kaina ba, na sanya kayana na zauna kwalam
babu komai sai garwashin wuta sai ko tuwon
dawa miyar kuka da Baba Rahina ta yi in ban
da shi ba a kawo min komai ba, ko mancewa
da jegon nawa suke yi oho? Ban saba irin shi
ba na tuna jego a gidan Kabir Modibbo a
daidai lokacin da na ji cikina ya yi kukan da

ya kara tabbatar min da cewar halalinshi yake so a bashi, na jawo kwanon tuwon nan gabana na bude shi da nufin ci, raina ya kara 6aci da na ga ko malmala mun tuwon wai ba a samu daman yi ba debo shi kawai aka yi da mara aka yaba min shi a kwanon ni kuma gani da wata sakaryar dabi'a bana iya cin abincin da bai bani sha'awa a ido ba ko da

kuwa dandanonshi mai dadi ne, na tuna Wada da irin dawainiyar da ya yi ta yi dani a lokacin da nake zaman renon cikinshi na cc ko in da na karbi haihuwar nan hannu bibiyi na haifan mishi wannan dan da Inna take ta magana a kan shi, ta kuma kwallafa ranta gare shi, tamfar bata taba samun jika ba sai a kanshi ko da wane irin tarairaya da dawainiya zai yi mun oho? Nan take na ji zuciyata karbi maganar tamfar dai da ita nake yi ko kuma ina bukatar amsawarta, fadi wal take yi Wada bai taba samun haihuwa ba ya kuma neme ta ido bude bai samu ba, sai a kan ki ya yi dace kuma ki ka haifan mishi da namiji da Inna take ta nanata kaman shi da ubanshi, ai

da kin yarda kin karbe ta hannu biyu to da ke kam kakarli ta. yanke saka, da kinga yanda ake tattalin mai jego tunda dai ya nuna miki shi gwanin tattali ne a zaman.renon cikinshi da kika yi, haka nan ya tattalaki sanda ya dora ki a shimfidarshi, nan da nan zučiyata ta koma tunano ranar tarewata gidan Wada dare na na farko a gidan shi daren da shi ne ya bayar da sakamakon da ya zamo shi ne

sanadin komai, daren da ya mantar dani niyyar da na tafi da ita cikin gidan nashi ya sanya ni na rinka gani da jin cewar dama can ni din tashi ce dama can shi ya cancanci ya. mallaki duk wani abin takamar da nake dashi daren da ya sanya ni a wani matsayı da ban taba samun kaina a ciki ba daren da.....na yi maza cikin jarumtaka na katse wannan tunanin don kuwa nasan bai da wani amfani a Wurina, in banda tayar min da hankali da zai yi.

Al'amarin Inna ya sake fado min na yi maza na tsallake kwanonon tuwon dake gabana a daidai lokacin da agogon wayata ya

nuna min karfe goma da rabi na dare, 3310 ce na tuna ranar da Wada ya kawo min wayar a matsayin wacce ya iya saya a dalilin sace min wayata mai tsada da aka yi a layin awon cikin da muka je, Inna ta gaya mishi ban yarda na tsaya yaánda aka yi na yarda na soma rike ta ba na nufi dakin Innan tun daga bakin kofarta na soma jin tana fadin, "waiyo kirjina, waiyo ji nake kamar zai fashe na yi maza naja da baya na tsaya ina fadin yau na shiga uku

kirjin Inna in ya fashe ni 'yasu yaya zan yi da rayuwata? Na tsuguna nan wurin ina ta kuka ina kuma jin Yaya Buhari yana fadin yi hakuri Inna rufe idonki kiyi bacci, na fi so sai gobe da safe muje asibitin don akwai Likitan da nake so ya duba ki, ta ce ai ba zan iya baccin ba ne da na rufe idona sai in soma ganin yaron nan gashi kuma jin zuciyata nake yi tamfar tana lilo na yi maza na kama fadin waiyo Allahna yau na gamu da gamona. Zuciyarki bata lilo Inna damuwa ce kawai ta yi mata yawa kuma yanzu ba dadewa za ki

samu saukinta rufe idonki in karanto miki wannan addu'ar da na saba jin Baba yana karan tata a duk lokacin da bacci ya kaucewa idanuwanshi, gyara kwanciya ki gani bari in gyara miki ruhuwarki, gyara Inna yi hakuri ai bai kamata ace ke mai bada hakuri kuma kin kasa hakura da bacin ran da ya same ki ba yana fadin hakan ya soma karanto mata addu'o'i ga abin da na ji yana karantawar. "Allahumma gahrahnnunjumu wa hada ahl uyunu wa anta Ha iyun kaiyumu lata'akuzuhu

sunatun walanau mun yah haiyu yah kaiyumu Ahadi ilaih wa anim aini.
Sau uku na ji shi ya karanto mata tana fadfi a bayanshi sai ya ce mata to karanta ke kadai in ji nan da nan itama ta yi tiryan-tiryan kamar dama can ta dade da sanin addu'ar, ba a dauki wani lokaci mai tsawon da ya wuce mintoci biyar ba sai kawai na jiwo saukan numfashinta alamar dai ta samu baccin. Nan take kuma sai ga Yaya Buhari ya fito daga dakin yana nufin tafiya gidanshi ya kalle ni ya ce "A cikin sanyin nan ki ke tsugune ga

jego? Ki dai rinka kula da kanki, ya wuce ni yana fadin kar ki samu damuwa tafi dakinki kawai Inna bacci mai ni'ima zata yi saboda darajar wannan addu'a da ta karanta."
Na dawo dakina na hau kan 'yar katifata na kwanta, fatana bai wuce nima bacci ya dauke ni kamar yanda ya dauki Inna ba nayi kokarin karanto addu'ar da na ji su suna karantawa don nima in samu baccin na kasa tamfar ba yanzu na ji su suna yin ta ba, na yi iyakacin kokarina wajen hada kalmomin da na ji suna fadan abin ya gagara har dai na

hakura na kwanta kawai na yi shiru ina tunanin abin da na sani na ilimin addini a rayuwata izu biyu ne kawai, sai suratul Yahsin, da Babana ya karantar dani maganin bacin rana da na ga wannan tunanin ba zai fisshe ni ba sai nayi maza na kavwar da shi na koma tunanin abin d aya hana i yin baccin yunwar dake kwakular cikina ne ko damuwar da nake ciki a dalilin rashin lafiyar Inna? Ko kuwa bakin cikin abin da Wada ya yi min na tafiya min da dan jaririna da ya yi?

Wastsakewa kawai ya kamata ki yi ki
hanzarta komawa gidan Kabir Modibbo ki
samu 'ya'yanki da daular da ki ka saba da ita,
Lari kuwa kya san artabun da ku ka yi ki ka
yi maganinta, ki ka dau fansa kan abin da ta
yi miki shawarar da zuciyata ta bani kenan.
A kanta kuma na ke ganin zantsaya
hanzarta komawa gidan Kabir Modibbo,
tunda dama ai manufar da ke zuciyata ke nan
manufar da na so cikarta tun watanni da yawa
da suka wucc cikin dan gidan Wada ya tsaida
ni, wanda bata lokacin da nake ganin cikin na
Wada ya yi min nema yasa na kau da kaina

da zuciyata daga son dan jaririn nashi, koma
can a binki, koma kije kiyi zaman 'ya' yanki ki
kuma ci daular da ya tara muku, koma ki yi
zaman ya'yanki, na ii ta tana ta yawan nanata
hakan, abin da ya ingiza ni ga tunanin
menene ma'anar zaman 'ya'ya? Ina yiwa kaina
wannan tambayar sai kawai na ji ta tana ta
jero min bayanai iri-iri daban-daban, abin da
ya sani nayi maza na tashi zaune a kan yar

katifar tawa don ni na tsaya jin bayanan da take shirin yi mun din zata jefani ne cikin halin da ba zata iya tsamo ni ba, don haka nayi maza na karanta kulhullahu uku na shafa a daidaiin da nake zaton nanne mazaunin zuciyarta tare da addu'ar Ubangiji ya yi min maganinta ya tsarkakace min ita, kar ya barta ta yi min irin abin da take yiwa sauran mutane, na kai su da take yi tana baro Su.

Har dare ya yi nisa sosai ban samu na runtsa ba abin da na gane kuma shi ne in dai har ina so in yi baccin to dole ne in nemi wani abin da na baiwa cikin nawa ya hakura, don haka na sake jawo kwanukan tuwon nan

na kawar da fuskata can gefe nufina wai in ci tuwon ba tare da na sake kallon shi ba, ina so ka yan yatsuna a jikinshi, na gane hakan ba zai yiwu min ba don cikin sauri na maida idanuwana gare shi ba tare da nasan lokacin da na yi hakan ba, ya riga ya sandare tuwon Inna ba ya haka, abin da zuciyata ta tuna min kenan, a hankali na tashi na fito waje rike da

kwanukan tuwon a hannuna kicin na shiga na hada ita ce na hura wuta na dora dumame ina jiran ya yi zafin da zan iya cin shi, ina tunanin rabona da hada wutar itace.
Na dawo dakina na zauna na gama cin tuwon na dan kwanta kamar ace zan samu bacci sai kuma na ji nonuwana suna motsi nayi maza na tashi zaune ina kallonsu wai zuba suke yi jaririnsú suke nema tunda nima na ciwa cikina to shima ya samu ya baiwa nashi cikin, to baya nan ba ya kusa, balle ayi hakan, na zuba musu ido na yi musu wani irin kallo matsananci, yayin da ruwan nonon ya ke ta tsartuwa har tsakar dakin.
"Ai wadannan nonuwan naki za su ishi jaririn da za ki haifan min ya koshi kuwa?

Raina girmansu nake yi gashi kuma ni nonon uwa zalla nake so yasha." Kalmomin Wada ne wannan a wani lokaci can baya da yake nufin zolayata, ina ma Wada da dan jaririnshi suna kusa da sun ga abin mamaki, da ya gane cewa yawan nono ba daga girman nonon ba ne, baiwa ce kawai kowa da yanda aka yi shi,

ban yi komai don haka nonon zuba ba, kallon su kawai nake yi ita kuwa zuciyata sai faman kuna take yi tana wani irin zafin da ba zan iya kwatantawa ba, ina ma dai ace nima na zamo mai hali irin na mahaifina kanmar Yaya Buhari? Gaba daya abin duniya baya cikin lissafinsu, suna son shi amma ba shi ne kan gaba cikin al'amarinsu ba.

Kar ka yarda ka zama mai yawan son abin duniya, kar ka zama irin mutanen nan da komai za su yi ba za su yi ba sai sun hango menene ribarsu? Me za su samu? Kayi iyakacin kokarinka ka rinka tantancewa tsakanin halal da haram kar ka zama mai yawan burin tara abin duniya ka sani cewa ita wannan rayuwa da ka ke gani in har akwai wani jin dadin dake cikinta to bai wuce

rayuwa ta tsaka tsaki ba, wacce baka sauka can kasa ba ba ka kuma haura can sama ba, wato baina-baina ke nan, in har ka samu abin hidimar iyalinka da sadar da zumuncin da ke tsakaninka da 'yan uwanka da taimnakawa daidai gwargwado to ka gama komai.

ina ma dai na dauki wannan nasiha dana taba jin Babana yana yiwa Yaya Buhari? Da ban samu kaina a halin da nake ciki ba a yau da yanzu ina tare da dan jaririna a nan dakin ina makale dashi a kirjina yana tsotson nonon shi dake ta faman zuba a karin kawai, da watakila ma Wada yana kusa yana fadin gyara mishi riko mana dan tallabe mishi kanshi, ya ji dadi da in ta dauro ma a gidan Wadan zan yi jegon tunda ba shi ba, ba Yaya Buhari ba, Inna ma da kanta wacce a can baya ni da ita ne muke da barin tara abin duniyar, ni da ita ne muke sha'awar daula, har ma in muka ji Baba yana yi wa Yaya Buhari irin wancan nasihar mukan dan kalli juna mu tabe baki in muna kusa ma muyi rada a tsakaninmu mu ce maza dai ya dauki irin wadannan nasihun nashi su haske mishi

zuciya, ya kasa neman na kanshi ya yi ta fama da dan tsukakken gida kamar zuciyar talaka, to itama ta watsar da wancan ra'ayin akan Wada ta roke ni in yarda mu maida aurenmu muyi zaman mu don shi din

kudinne kawai ba shi da su amma komai na cikar dan adam yana dashi kuma shima ba babu ne karkaf ba don in na lura da irin hidimar da yake yi tun daga 'ya'yan itatuwa da yake kawo min da hidimar gidan da ya dauke zan gane yana samu a sana'ar tashi ta shayi na yi kememe na ki saboda tunanin yaya za'ayi in zama matar mai shayi in na gaya mata hakan kuwa takan ce to na nawa? Wai an tambayi tsuntsu me sunanka? Ya ce na nawa? Matar me shayi kam ai kin zama sai dai kar a kara tunda ga cikinshi nan a jikinki kina fama dashiki tashi da kyar ki zauna da kyar watakila ma da a gidan nashi kike da bai yi miki nauyi haka ba naki kula zancen nata na yunkura na tashi na koma dakina saboda sanin abin da take nufi da maganar tata da na yi.

Wada ta samu so mai yawa a wurin lnna da Yaya Buhari, a dalilin kyautatawa da girmamawar da ya yi ta yi musu tare kuma da kyakkyawar mu'amalla da ya gudanar a tsakaninsu ta yau da gobe sai daini kam bai

yi nasarar samun kaina ba boda raina, sana'arshi da ya yi a duk lokacin da ya yi mun tayin to ko zai canza wata sansar ne in har bana son shayin? In na soma tunanin in ce mishi eh kafin in gama in bashi amma sai ya. fara lissafo mun wai sana'o'inda ya iya wadanda wai cikinsu ne zan zar mishi, ya soma fadin ai kinga na iya wanki da guga, na iya aski na iya danbe na iya yankan farce, na iya shoe shina, yanzu takalmin nan naki mai kyau da ki ka wulakanta. shi ta hanyar sanya shi a ruwa saboda ba ki san zafin kudi ba da zan dauko akwatina na kayan gyara da na mayar miki dashi sabo, ya dauki takalmin a hannunshi ya rinka kwatanta mu in zai gyara shin yanda zai yi mishi sai ya gama ya maida shi ya ajiye in ya gane ko kallonshi bana yi balle in saurari bayanin nashi.

Shi da kanshi Wada ya gane sana'arshi ita ce ta fi komai kawo mishi cikas a wurina, don ya taba bina har dakina a ranar da ya zo gidan ya samu Inna bata nan, yana shiga dakin ya Soma yi min magana cikin marairaita yana

fadin.

"Haba Rahina, ki ji tausayin zafin da zuciyata take fama da shi a kanki mana, don me za ki yi ta azabtar dani? Shi talaka wai bai samun abin da yake so ne? Aure ni don ni din mana aure ni don abin da ki ka gani ki ka kuma sani game da ni."

Na yi maza na galla mishi harara, na ce "Me na gani? Kuma me na sani? Ina fadin haka ya yi maza ya kwabe zulunbun janfar da ke jikinshi ya jefar ya ce ai kin taba ganina in kuma dadin baki kalle ni da kyau ba to gani yanzu a gabanki kin kuma san a ko ina zan iya rike ki zan iya ciyar dake nauyin abincin da kike bukata ko wane iri ne, kuwa in muka kebe kuma zan jiyar da ke irin shi ina son ki Rahina, ba kuma ina sonki don wani abinki ba ne, ina sonki ne don ina sonki, ina sonki tun farkon ganina da ke in ban da haka da ban

yarda da zola yar da kika yi min kan maganar auren ki ba, don tun farko nasan manufarki ni kuma da ki ke kallona ba kowa ce macc nake mikawa kaina ba don haka taimake ni kiyi

min irin son da nake yi miki, shi ne so tsantsa wanda babu algus ko mahadi ko wani dalili a cikinshi, ni da ki ke kallona a kowanne hali mutum ya kasance zan iya zama dashi matukar dai shi din shi ne abin da zuciyata take so ba na miki fata amma da zan ganki cikin wani hali zan iya zama da ke don ina sonki.

A A lokacin da yake yi min wadancan maganganun ko kallonshi bana yi balle ya gane ina jin abin da yake fadi.

Na sake yin kokarin dawo da tunanina in da nake zaune ban son yawan tashi a dalilin na ji an ce wai har dashi cikin abin da yake haddasawa mutanen wannan lokaci lalurar hawan jini, na yi maza na sake tambayar kaina ko yaya za'ayi dan adam a yau ya fita daga cikin tunani? Na kalli al'amarina da matsayin shekarun da nake ciki kasa nake da talatin kwarai amma ga halin da nake ciki da

damuwar da ta same ni, to in dai kamar yanda nake zato ne yawan shekaru yawan tunani tunda naji ana cewa komai hankali da

natsuwar yaro ba zai iya hango abin da babba ya hango ba, ko da kuwa bishiyar rimi ya hau, to ai kenan al'amarin yana da girma.
Na gyara da nufin in dan kwanta a kan 'yar katifar nan ko zan samu in dan runtsá musamman ma da yake babu wani motsi da nake jiwowa ko'ina shiru ne a dalilin dare ya yi nisa, ina kai kafada ta akan katifar na ji ta a, jike sharkaf kamar an zuba mata ruwa, ruwan nono ne kasa, hana kaina kuka na yi na ce waiyo Allah na waiyo Wada, a irin soyayyar da ka ce kana yi min menene ya sanya ba ka sanya tausayi a ciki ba, da kana sona kana jin tausayina da ba ka tafi min da yaro ba.
Ankara na gane gari ya waye ba, sai da na ji shigowar Yaya Buhari cikin gidan nan, nan da nan kuma sai gashi an fito da Inna asibiti za'a kaita da sauri na tashi na fito waje har sun ja mota sun tafi na yi maza na bi bayansu a kan babur zuwa asibitin da suka nufa,

gwajin farko da Likita ya yi.mata akan idona ya cewa Yaya Buhari har da hawan jini cikin

damuwar tata shi ne ma ya fi komai don ya hau da yawa, na ce na gamu da gamona ni Rahina tawa ta same ni, kukan da nake yi shi ne ya yi dalilin da aka koro ni waje nazo na zauna gindin wata bishiya mai yawan ganye ina tunanin al'amuran da kullum a cakalkale suke maimakon su rinka gyaruwa sai kara caccakalewa suke ta faman yi.

Ina zaune a wurin na soma tunano mahaifina sanda yake raye yake tattalin ganin na girma na zama mutumiyar kirki kuma mai dogaro da kanta bai kaini makarantar boko ba sana'ar dinki ya kaini in koya da nufin kan in isa aure na iya. Ina isa kuma sai ya aurar da ni kowa ya huta, da ya samu ikon aiwatar da wannan buri nashi a kaina to da ban zamowa Inna sanadin da na zama mata ba a yau, a dalilin wata ja'irar matar kabila dake yawan zuwa shagonmu na bijirewa koyon dinkin saboda kullum tazo shagon ta ganni ina fama da zare da allura ina dinkin rigar takarda ina soke hannuna sai ta ce min "come on throw

away that thin most you beautiful once suffer

before you survive? Ma'ana wai in jefar da wannan abinda ke hannuna dole ne har mu ma kyawawa sai mun wahala kafin mu rayu? Da wannan abin da ke hannuna dole ne har mu ma kyawawa sai mun wahala kafin mu rayu? lun tana fadi ban san me take nufi ba har dai rannan aka fassara mun bata taba shigowa shagon mu ba tare da ta dafa kafadata ba, haka nan bata taba dafa kafadar tawa ta wuce bata fadi wadannan kalamanba, har da hakan yasa na yi wa dinkina rikon sakainar kashi wanda ya yi dalilin da aka dakatar da ni aka ce wai sai wani babba yazo daga gidanmu. Shi kuma Yaya Buhari ya ce da yaje shago bada hakuri ya ce da zaje shago ba da hakuri gara ya kaini makaranta in yi karatu tunda dama shima ba a son ranshi nake koyon dinkin ba, kaini makaranta da aka yi shi ya zamo tushen komai a can na gamu da Lari, Lari ce tushen komai da nake ciki a yau dama wanda Inna ta samu kanta a cikin kome zan yiwa Lari in rama abin da ta yi mun? Ita ta yi dalilin da makarantar da aka kai nin ban

samu takardar shaida ko guda daya ba, ta yi dalilin da na yi auren da babu mai so saboda rashin halaccinshi sai dai anyi shi ne kawai don a rufa asiri a daidai lokacin da aka gyara auren nawa na kuma son zaman saboda dalilai masu yawa, ta kuma yi sanadin fitana ta shiga ta mayye gurbina, har da takaicin wannan abin da burina na daukar fansa a kanta ya hana ni'yin auren da zai dace dani shi ne auren Amiru, da Amiru na aura da wannan abin bai faru ba, sai na auri Wada ido rufe kan wata manufa, da muka yi auren kuma sai na kasa bude idanuwana in hangowa kaina cancantar da aka hango min ina ma dai na bude idona na hangi cancanta da yanzu ina tare da Wada da dan jaririnshi da wannan abin bai samu Inna ba a yau. In na dunkule abin kuma gaba daya na hada shi wuri daya sai in ce Larin ce dai sanadi. Mu'amalla da ita ne ya sani nake iya musu da kowa ma ciki har da iyaye don bata maida nata a bakin komai ba, biyar da suka yi mata da tsoronta da suke ji ita bata yi musu rabin-rabinshi a dalilin haka na lalace sai nake

ganin ai ni nawa da kyau ai ba zan iya yi musu irin yanda take yi ba, amma in ban da haka in banda na iya musu da iyaye ai da na auri Wada irin magiyar da Inna ta yi min a kanshi ba sana'ar shayi ba kuwa ko da dan bola ne don shima Wadan ya taba tunzura kan magiyar da Innan ta taba yi min a kanshi a gabanshi ya roke ta tasa baki cikin maganar tamu ta yi maza ta yi td roko na har ta gaji ta yi shiru ban tanka mata ba, ya kalle ni cikin natsuwa ya ce.

"Me na yi miki haka? Me yasa ki ka tsananta al'amari a kaina? Ba Inna ce ta haifan ba, amma ba za ta yi min daya bisa goman rokon da ta yi miki ba, zan yi mata duk abin da take so in yi mata ko da kuwa menene tsananinshi?"

Na bude baki da nufin ba shi amsa, sanin da ya yi banzar magana zan gaya mishi yasa ya yi maza ya kuza min ruwan sanyin randar Inna da ke hannunshi cikin kwanon sha a fuskata, sai da na nemi shidewa saboda yawan ruwan da sanyinshi gashi kuma ban yi zaton zai iya yi min irin hakan ba,

musamman da yake a gaban Innan muke zaune, ita kuwa sai ta. yi kamar bata ga abin da ya y1 ba, da ya koma ya debo mata wani ruwan sai kawai ta karba ta yi abin da zata yi na yi ta kuka saboda takaicin wulakancin da ya yi mun din ba ta ce min komai ba shi kuwa sai ya shiru silifas din shi ya fita ya bar gidan.

A yau ina takaicin al'amura masu yawa tare kuma da sanin cewa, hanyoyın da nake dasu na gyara kadan ne bani kuma da tabbas akan yiwuwar nasararsu.

A duk lokacin da na tuna al'amuran da na kuskure a baya na kan ji jikina ya yi sanyi musamman al'amuran da suka danganci Wada mai shayi, tunda shi ne da nasan ya bini bi na zahiri na kuma yi komai don in nuna mishi bana yi dashi ba kuma zan yi dashi din ba, sannan shi ne mutumin da na san Inna ta nunawa so itama a zahirı har ma ta yi ta gaya min kalmomi a dalilin bacin ran kiyaiyar da na nuna mishi, bana manta ranar da ta ji shi yana rarrashina yana fadin kai ni Wada, ni Wada tawa ta same ni, na kuma

gamu da gamona kome na yi wa Rahina a rayuwa? Oho. Rahina ki soni mana mu maida aurenmu, don in samu damar da zan nuna miki ina sonki irin son da ya dace in girmamaki irin girmamawar da ta dace dake in miki duk wani abin da nasan kina so kinga dai tunda nasan ke mai bukatar mota ce muna maida auren zaki je ki zabi. irin wacce ki ke son hawa ba ma irin wannan takin ba don wannan ba jib ba ce kafi kura gudu sunanta, ba zan damu ba in sai miki dalleliyar mota ki hau ni kuwa in rinka taka kafafuna ina zuwa shagon shayina ina sana'ata, inda zan samu abin da zan rinka biyan masu adashe-adashen su.

Na kalle shi na ja mummunan tsaki, na kuma dalla mishi uban harara kafin na ce mishi "Jarin nawa ne a cikın shagon shayin naka da har ka ke cewa wani wai zaka saya min dalleliyar mota? Kuma motar tawa da kayi min sanadinta ne kafi kura gudu? To dadin abin dai ba ka da kamarta sai alkawarin karya." Inna ta yi maza ta ce min "Ke kul

bana son diban albarka, Wada ya yi

murmushi ya ce kyale ta Inna ya sake juyowa gare ni ya ce to na ji kin yi sa'a kin gane alkawarin karya zan yi miki na kuni sani dama bani da komai, to amma ina sonki aure ni don son da na ke yi miki, na yi miki alkawarin zan kare miki mutunci in kuma girmama auren ki, ina ce shi kenan wannan shi ne babban abin da ya kamata mace ta nemi samu a wurin mijin aurenta." Inna ta y maza ta ce "Shi ke nan kuwa sai da1 in ba auren take nufin yi ba."
Wajen awa biyu ina zaune a gindin bishiyar nan kafin Yaya Buhari ya fito yazo ya same ni, muje gida kawai sun kwantar da ita, sun bata gado Baba Rahina ce zata.zauna tare da ita, saboda ke din ba ki da karfin jiki kema kina bukatar a kula dake ne, ba ki kula da wani ba, na ce amma da ni ka bari na zauna da itan da zai fi, ya ce a'a muje gida ba ku da fahimtar juna a yanzu ba zan bar ki wurinta ba, don kar ta zo tana ganinki tana

tunawa da bacin ranta, kina dai ji an ce
hawan jini ne kan wannan dalili ne yasa na

yarda na biyo yaya Buhari ya zo ya sauke ni a
gida.
Kullum na kan je asibitin da safe sai dai
ban cika jin dadin zuwan ba, don Inna tana
hango ni take runtsc ido in zan gaishe ta
kuma sau goma bata amsawa a gaban kowa.
kuma abin da take yi min kenan har a gaban
Amiru da kullum shima sai ya je, kuma ni
dashi ba ma kula juna tunda na auri Wada ya
daina magana da ni, nima na daina kula shi
sai mu hadu mu rabu babu mai cewa wani ci
kanka, da kuma wani a wurin zai ce Inna
Rahina tana gaishe ki, ba ki ji ba, sai Baba
Rahina ta yi maza ta ce "Haba kyale ta kawai
tana ji bakin cikinta ne ya isheta, wannan 'ya
da ki ke gani in ka biye mata aman zuciyarka
zaka yi, ace dai so irin wanda Maude take yi
mata so har da na sahalci ta kure ta ta cika
mata ciki ai kuwa kin san babu hali, kema
duk a zuba min ido ana kallona ana fadin sai
hakuri, wannan dalili yasa na daina zuwa

asibitin na koma zaman gida ni kadai
kwalam, babu kowa sai ni sai tunane-tunanen

da na kulla abuta dasu don a yanzu su ne
manya abokaina.
Rannan da safe ina zaune a gida ni kadai,
bayan na kammala ayyukana, ranar kuwa
kwana bakwai ne cif da haihuwata da jaririn
yana tare danl, to da ranar su na ce yau to
amma ko da bai tare dani yau dinne dai ranar
sunan nashi yau ne ranar da zai amsa
sunanshi in dai har yana raye ko menene
sunan da za'a sanya mishi?
Tunanin da ya zo zuciyata ke nan ban sani
ba, na tuna hirar Wada Mai Shayi da Inna
ranar da ta roke shi ya sanyawa jaririyar da
zan haifa sunan mahaifiyarta, ya yi murmushi
ya ce "To Inna in har ta zamo macen zan iya
yin hakan duk da dai nima ina da tawa uwar,
ina kuma son sunan nata, to tunda ba mace
Wada ya samu ba ina jin sunan mahaifinsh
zai sanya ko kuwa wanı babba daga cikin
zuriyarsu, ko meye sunan mahaifin nashi?

Ban taba neman sani ba na dan yi tunani kadan kafin na ce watakila kuma ya yi min kara ya sanya mishi sunan nawa uban Aliyu,

don haka sai na yankewa kaina shawarar to bari nima kawai in rada wa jaririn' suna in kira shi Abba a hankali na bude baki na fadi Abbana har na dan yi murmushin jin dadin danganta shi da jikina, da na yi ko da ban yarda na kalle shi ba balle in ganshi sonshi nake yi1 So kuma mai tsanani na gane hakanne a dalilin bana minti biyar al'amarinshi bai dawo min cikin raina ba, sannan a duk lokacin da na tuna shi tsananin tausayinshi yana kama ni in kuma tambayi kaina ko wanne hali yake yanzu?
Ido biyu ko yanà kuka don bukatar abincin shi? Oho, sai kuma in yi shiru in kama tunanin ina Wada ya shiga da yaron nan? Ko su iyayen nashi wadanne iri ne da zai kai musu jariri su sa hannu su karba ba za su ce mishi yaje ya kaishi gun uwarshi ta shayar da shi nono ba? Da dai ina da hali a wannan loka ci to da na shiga duniya neman Wada don in

karbo dan jaririna in dawo dashi in kaima
Inna shi ta ganshi ta ji dadi hankalinta ya
kwanta hawan jininta ya sauka, nima in samu
natsüwar zuciyata, in samu farin ciki da

nishadin dake cikin mu'amallar uwata danta
na shayar wa da reno wanda shi ne jagora na
shakuwa da soyaiyar da ke tsakaninsu.
"Assalamu alaikum." sallamar da na ji ke
nan na dago kaina daga sunkuyon da na yi
ina sauraron hirar da muke yi ni da zuciyata.
"Wa alaikumus salam." Na amsawa
saurayin da ya yi sallamar naso in gane shi,
amma na kasa tunawa da shi sosai har sai da
ya karaso inda nake zaune ya tsuguna yana
gaishe ni, sannan ne na gane shi da sauri na
ce mishi, "A'a, Sirajo kai ne ka zama haka?
Ka wani zama kamar uztaz, ka zama mai
tsabta da kyan gani, ka yi haske ka yi kiba,
kamar ba kai ba? In ce ko wata duniyar ka
shiga ne ka samu dadi a cikinta?" Na dan yi
mishi murmushi saboda tsohuwar sanaiyar da
ke tsakaninmu kasancewar yayan makwabta
don gidajen mu nisan da ke tsakanin su ba

mai yawa ba ne, ban da haka kuma ni da shi mun taso ne kusan a lokaci daya ina nufin banbancin da ke tsakanin haihuwar mu ba mai yawa ba ne, don mun sha yin fada ma sanda muke kanana a makarantar alló ko a

wasannin maza da na kan y1 karambanin shiga.

Duk da wannan mu'amallar dake tsakaninmu sai naga wai nema yake yi ya girmama ni don haka na zuba mishi ido ina sauraron abin da ya kawo shi, hankalina dai a kwance duk da ni kadai ce a gidan, don ban ganshi cikin kamannin da na saba ganin shi ba, na shaye-shayen miyagun kwayoyi.

"Anti ina wuni?" Cikin raina na ce babbar magana, ni da aka saba kundumawa ashar yau ni ce Anti? Ban nuna damuwa ta ba a zahiri, sai na amsa lafiya lau Surajo, kana nan lafiya? Ya celafiya lau, Yaya jikin Inna? Na ce mishi da sauki sosai, ya ce eh naga alama don nima na je shekaran jiya, da jiya yau ma za ni in an sauko daga Masallaci, na ce to an gode ina dai ci gaba da sauraronshi.

"Wanki na zo ki bani in je in yi miki, don

dama da Mallam Wada yake karban kayanki ni yake kaiwa in wanke in goge, a kawo miki bayan na goge su, shi ne na ce bari in zo in karba don na yi tunanin sun taru."

58

Na ce "Lah! Babu komai Sirajo, ai ya riga ya tafi babu maganar yin wanki da guga, kuma tunda ai dama shi ne mai biyanka ko? Ya ce "Ko ba ya nan zan ci gaba da yi miki wanki, da guga, ba don ku biya ni ba sai don in ji dadi cikin raina, don nasan na yi wa ubangidana da na rasa wani abin da zai ji dadi inda zai sani, na daga ido na kalle shi a diadai lokacin da ya kara sunkuyar da kanshi kasa ya ce "Umarnin da ya bani na in girmamaki shi ne ya kawo ni gabanki a yanzu in ban da haka da ba zan taba ganin mutuncinki ba, don kin yi sanadin rabuwata da shi a lokacin da nake bukatar shi, ba kuma ni kadai ba ne muna da yawa irinmu-irinmu wadanda Mallam Wada ya yi sanadin shiryuwarmu ya raba mu da shan wiwi, ya hana mu zarman banza ya yi mana sanadin sana'a ya maida mu makaranta don mu yi

ilimi ya sasanta rashin jituwar da ke
tsakaninmu da iyayenmu, ya kuma koya
mana tarbiyar zaman duniya, amma mun rasa
shi yanzu a dalilin ki, sai dai duk da haka
zamu girmama ki zamu miki ladabi da

biyaiya irin wanda muke yi wa iyayenmu a
yau, domin abin da ya gaya mana ke nan a
duk lokacin da muka tuna dashi mu
girmamaki, na kuma san ya hada mu da
wannan aikin ne saboda fusatar da muka yi a
lokacin da ya tara mu ya yi bankwana damu
da muka tambaye shi dalilin tafiyar tashi bai
boye mana ba.
"Muka ce mishi ina runwaka da ita
Malam? Bayan ka riga ka samu ka gama da
ita? Ba danka ta haifa ba? Wane fiffika kuma
a yanzu ta yi maka? Da ita da wannan fadin
ran nata da jin da take yi ita din wata a bace
ka samu ka shimfide ta a shimfidar ka har
kuma sakamakon hakan ya baiyana wa kowa
da kowa tunda ga da nan ka samu a tare da ita
kashedi kawai zamu yi mata da ita da dan

uwanta na su canza hanya kar su rinka
biyowa ta nan balle ka rinka ganinsu kana jin
babu dadi."
Sai ya kalle mu ya yi murmushin karfin
hali ya ce, "A tunaninku da na wasu za ku ga
cewar tunda na samu damar da na dora
Rahina a shimfidata na kuma samu damar

dandanar zumanta shi kenan zance ya kare,
bani da wani gigitaccen kwadayi a kanta to
hakan ya kamata ace al'amarin ya zamo min
sai dai kuma ba hakan ya ke ba a wurina,
aurena da ita ya taradda ni ne kan
matsanancin sOn da na rinka yi mata, a tun
farkon zuwana garin nan maimakon in samu
saukin al'amari sai na zama tamfar dandani
haukaci aka yi min alherin da na samu a tare
da ita kuma ya tilasta zuciyata girmamata duk
da azabtarwar da take yi mata da na tabbatar
da bata da bukatar ci gaba da zaman aure tare
dani to babu abin da ya kamace ni illa yin
nesa da ita, al'amuran ta zan fi mun kyau in
koma ta inda ba zan ji labarin ta ba, ba za ta j1
nawa ba don kar kishi ya debe ni in aikata

abin da ba zai yi dadi ba, tunda nasan nan ba dadewa ba zata yi dayan biyu, in ma dai ta koma gidan tsohon mijinta da ta yi amfani da ni wajen gyara aurensu ko kuma ta yi wani sabon auren kowanne ta yi a cikin biyun ba mai dadi ba ne a wurina, ina kuma tabbatar muku da cewar dole ce kawai zata faba ni da ku, ina son ku ina jin dadin zama da ku

saboda kuna debe min kewar al'amura masu yawa, samunku da na yi shi ne ya yi dalilin zamana a nan na dade har ga shi kuma a dalilin hakan na samu wani babban alherin da na dade ina nema shi nc zuriya, don haka al'ama rin komai muhimmanci ne a wurina, zan yi sallama da ku a yau tare da rokon arzikinku kan cewar Rahina ta zama abin girmamawa a wurinku, a duk lokacin da ku ka tuna da ni saboda nima ina girmamata, ya dago ya kalle ni ya ce min, "Wannan umarni da ya bamu shi ne dalilin zuwana wurinki don tun safe na tashi da damuwar rashin ganinshi saboda mas'ala ta same ni wacce da ya na nan da tuni na tafi wurinshi na gaya

mishi ita ya gaya min abin da zan je in yi, to bayanan ban kuma san in da zan je in same shi ba, sai na ji zuciyata ta kuntata kwarai da abin da ki ka yi mana na sanadin rasa shi da ki ka yi, don haka nazo ki ba ni kayanki in je in wanke miki su in goge in kawo miki ko dama can nine mai yi miki saboda ni dama a sana'o'in da ya raba mana ni wanki da kuka ya ce in yi shi kuma nake yi na kuma same ta

a yanda ya gaya min ita cewar sana'ace da aka raina ta, amma kuma akwai rufin asiri mai yawa a cikinta, na kuma gani tunda a yau da ita nake biyan kudin karatun da nake yi wanda shi ya saman min makarantar ya kuma dauki nauyin komai na fara karatun nawa daga nanne ya ce min to ga sana'a in riketa don in ci gabi da rike kaina, maimakon jiran sai wanı ya yi min babu mai son yawan bukatu in dai ba Ubangiji ba ne"
Na zubawa Sirajo ido ina kallon shi cikin sanyin jiki na rasa me zan ce mishi? Hakuri zan ba shi kan bashi da ubangidan shi da ya ce na yi ko kuwa jan bakina kawai zan yi in

yi shiru in je in kwaso wankin da ya zo karba in ba shi ya tafi? Ban saru ba.
Tsawon lokaci ina cikin tunanin kafin na bude baki na ce mishi, "ka yi hakuri Sirajo, yau kam bani da wanki kuma ba ma sai ka rinka baro wajenka kana zuwa karba da kanka ba, in suka hadu ni da kaina zan daure su in bayar a kawo maka, ya ce mun to ya mike zai fita ya ci karo da bokiti sai kawai ya sure shi ya fita dashi yana ta jido ruwa yana

ciccika randuna, na ce Sirajo mu masu tsohuwar rijiya a gida ka wahalar da kanka da diban ruwa ya ce, "Ai babu komai, ko me kyan ruwa rijiya ai ina ganin bai yi ya na famfo ba, ya yi ta jidon ruwan nan sai da ya cika duk wani abin da ya gani hatta kwanukan shan gidan sia da ya jera su ya cika su da ruwa ya rufe sannan ya fita ya tafi ina kallonshi.
Bayan fitarSurajo.babu abin' da ban tuna ba na al'amarina da Wada, in ban da umarnin kyautata mun ya baiwa su Sirajo ko da wane irin abu ne zai faru tsakanina da su oho.

Sirajo yana fita tamfar jira ake yi ya bar gidan sai ga wasu yara sun shigo su biyu suna rike da wata katuwar kwalla mai alamar nauyi, suka gaishe ni suka ce wai gashi mu kawo gidan nan in ji wasu mutane a waje." Na tashi naje na bude kwallar soyaiyan naman rago ne a dankare a ciki ga dukkan alamu ma ba a dade da gama soya shi ba, na wuce na nufi zaure in da aka ce wai mutanen suna tsaye. Su biyu na tarar suna ganina suka tafi kasa, suka zazzauna barka da fitowa Anti, an

samu kai lafiya? Na ce lafiya kalau, ina kallon su kan in ce musu komai sai su ka ce "Naman rago ne muka kawo miki don ki tada komada ga ma kai da kafar ragon nan mun miki gandanshi kuma ya yi laushi sosai, nan kuma yajin daddawa ne 'a ciki, tunanin da muka yi na cewar duk inda maigida Wada yake yau zai radawa danshi suna shi yasa muu ma muka yi mishi abin da muka ga zamu iya min nemi Malamai makaranta Alkur'ani sun karantawa yaron Alkur'ani sun yi mishi addu'ar Ubangiji ya raya shi ya kuma sa shi

din magajin ubanshi ne, ke kuma muka sai miki rago muka soye miki shi muka miki yajin daddawa da ganda muka kawo miki don mun san ana cewa kNankwason ragon sunan yaro na mai jego ne, to baya kusa balle a kawo miki kwankwason ragon radin sunan, don haka muka ga bari mu kawo miki ragon sukutum.

Na yi shiru ina nazari da tunanin zuwa can sai na ce musu bana son irin wannan abin da ku ke yi min, bana so kuna shiga cikin harkata aurena da Wada kuma ba ku ku ka

daura min shi ba, ban ga kuma abin da ku ka hada da shi ba da ku ke nema ku takura min hada baki suka yi suka ce min mu kuwa mu muka hada wani abú da shi tunda yan uwantakar Musulunci ta hada mu ban da haka ya zo ya shiga harkokin mu ya yi mana abin da iyayen mu suka kasa yi mana." Daya yaron ya yi maza ya cire hular sanyin da ke kanshi, wani saftarcren dinki ya raba kan nashi gida biyu sai da na ji tsoro, ya maida

hular ya gyara ta sannan ya kalle ni ya ce min, "Ni da dan sara suka ne har kirari ake yi min ana kirana tunkiya uwar danyen kai saboda duk wanda naga dama zan sarawa takobi, maigida Wada ne ya yi sanadin da na daina ya bani shawarar shiga makaranta in yi karatun addini saboda rayuwar da babu addini a cikinta rayuwar banza ce, ya bani shawarar kama sana'ar aski da yankan farce ya kuma bude min shagon ya gyara min shi ya sanya min kayaiyakin alatu na kiran kostomomi da kuma na aiki, a tun bara ya yi min aure yanzu haka ina da yarinya watanta biyu sunanki ma ya sani na sanya mata da na

samu kai lafiya? Na ce lafiya kalau, ina kallon su kan in ce musu komai sai suka ce "Naman rago ne muka kawo miki don ki tada komada ga ma kai da katar ragon nan mun miki gandanshi kuma ya yi laushi sosai, nan kuma yajin daddawa ne a ciki, tunanin da muka yi na cewar duk inda maigida Wada yake yau zai radawa danshi suna shi yasa mu ma muka yi mishi abin da muka ga zamu iya

min nemi Malamai makaranta Alkur'ani sun karantawa yaron Alkur'ani sun yi mishi addu'ar Ubangiji ya raya shi ya kuma sa shi din magajin ubanshi ne, ke kuma muka sai miki rago muka soye miki shi muka miki yajin daddawa da ganda muka kawo miki don mun san ana cewa kwankwason ragon sunan yaro na mai jego ne, to baya kusa balle a kawo miki kwankwason ragon radin sunan, don haka muka ga bari mu kawo miki ragon sukutum.

Na yi shiru ina nazari da tunanin zuwa can sai na ce musu bana son irin wannan abin da ku ke yi min, bana so kuna shiga cikin harkata aurena da Wada kuma ba ku ku ka

daura min shi ba, ban ga kuma abin da ku ka hada da shi ba da ku ke nema ku takura min hada baki suka yi suka ce min mu kuwa mu muka hada wani abú da shi tunda 'yan uwantakar Musulunci ta hada mu ban da haka ya zo ya shiga harkokin mu ya yi mana abin da iyayen mu suka kasa yi mana." Daya yaron ya yi maza ya cire hular sanyin da ke

kanshi, wani saftareren dinki ya raba kan nashi gida biyu sai da na ji tsoro, ya maida hular ya gyara ta sannan ya kalle ni ya ce min, "Ni da dan' sara suka ne har kirari ake yi. min ana kirana tunkiya uwar danyen kai saboda duk wanda naga dama zan sarawa takobi, maigida Wada ne ya yi sanadin da na daina ya bani shawarar shiga makaranta in yi karatun addini saboda rayuwar da babu addini a cikinta rayuwar banza ce, ya bani shawarar kama sana'ar aski da yankan farce ya kuma bude min shagon ya gyara min shi ya sanya min kayaiyakin alatu na kiran kostomomi da kuma na aiki, a tun bara ya yi min aure yanzu haka ina da yarinya watanta biyu sunanki ma ya san1 na sanya mata da na

tambaye shi sunan da za a saka mata in ban da shi meye gamina da ke? Dà har zan saka wa 'yata sunanki? Ni in ban da kar in yi masa butulci ma da ban canza sunan ba? Tunda kin yi dalilin raba mu dashi."Yana maganar yana fadin eye, eye, yana kuma motsa kafadu alamar dai shi din ba karamin iskanci ya tata

ba, kamar in tambaye shi dalilin haduwarsu
da Wada sai naja bakina na yi shiru, shi kumma
kamar ya gane hakan sai na ji ya soma cewa.
"Farkon zuwan maigida Wada garin nan ai
ina kan ganiyar amsa sunana ne na tunkiya
uwar danyen kai shagon shayin shi nake
zuwa in ce mishi a hada min indomi guda
uku da kwai hudu a soya min, a kuma miko
min biredi da kofin shayi don bana zuwa sai
na sha wiwi na ji ta yi ta yi min karo ta rarake
ni ta kuma sai ya gama hada mun na ci na yi
gyatsa mai karti sannan na ke mikewa in ce
mishi "To Wada mai biredi na ci na koshi na
yi gyatsa kudinka kuma karfi ya ci daru ya
danne in kuma kana ganin kamar kai din
namiji ne, to ka biyo hanya ka karba." Sai ya
ce min a'a je ka kawai tunkiya na bar maka in

kana bukatar ganin maza zaka gamu da su a
hanya, amma ni ba namiji ba ne don haka
bana bukatar tashin hankalı, neman kudina ya
kawo ni garin nan." Wannan cin bulus din da
na samu a wurinshi, shi ya sanya ni yin
tunanin to bari in rinka zuwa ina karbe mishi

kudin shagon nashi, rannan sai da na ci na koshi sai na ce mishi miko min na sigari in kana son zaman lafiya, sai ya kalle ni ya ce mun, "Haba tunkiya, ka ci kayana ba ka biya ba sannan in baka na sigari? Ai sai ka karya min jarin nawa, don haka kawai ka tafi." Na ce mishi, ba za a tafin ba zaka bani ko sai na Ci kazanka na soma kurma mishi ashar bai kula ba yanata kokarin sallamar kostomominshi.

Wani mutum a wurin ya mike yana bani hakuri don in kara tsoratar da maigida Wada sai kawai na kwashe mutumin nan da mari na kuma yi maza na tuntsurar da teburin shayin da mutane ke zagaye dashi, maigida Wada ya fito yana fadin "tunkuya za ka watsa min mutane ne? Yana yi min tambayar na dago hannu da nufin danbara mishi naushi sai

kawai ya cafke hannun nawa ya yi mun wani irin wawan duka a habata, ban sake sanin halin da nake ciki ba, sai da sanyin asuba ya buge ni sant:an na tashi na lallaba na tafi gidanmu, tun daga ranar ban sake zuwa

shagon maigida Wada shan shayi ba, don na dauka dama tsoro na yake ji, shi yas a yake bani, to yanzu kuwa tsoron ya gushe don haka ko naje ba zai bani ba, ina cikin haka rannan sai ka gamu dashi a harya ina kokarin 6ace mishi sai ya kwala min kira na tsaya ya zo ya same ni ya de mun "Yaya kwana biyu kuma bana ganin ka? Ai dan wannan abin da a ka yi ba zai hana ka zuwa kasha shayin ka ba, in kuma ka gama ka yi gyatsa ka yi bayanin ka babu komai kai dai kawai ba zan yarda ka taba mutuncin kostomina ba iyaka kawai kenan."
Da haka maigida Wada ya ja ra'ayina zuwa gare shi na zama ina jin kunyarshi, ina kuma girmamashi ta dalilin haka sai ya yi sanadin alheri mai yawa, to kin yi dalilin rabuwarmu da shi ke in ban da cewar da ya yi in mun tuna da shi mu girmama ki ba sai mun

yi sanadin da ku ka saida wannan tsohon gidan naku ku ka bar unguwar ba? To ya ce mu girmama mishi ke mun kuma yarda zamu yi hakan."

Na ce, to na gode." Nasa hannu zan dauki bokitin yajin daddawan suka yi maza suka sunkuce kayan suka shiga dashi har cikin gida, suka ajiye suna hada ido da bokitin sharar gidan mu suka yl maza suka sure shi suka tafi suka zubar, suka dawo da bokitin sai da suka wanke shi sannan suka maida shi wurin zuba sharar suka ajiye shi suka kakkabe hannu suka yi min sallama suka tafi, na zauna ina tunanin Wada, wato shi daj a rayuwarshi ya iya mu'amulla da 'yan iska ko kuma kangararrun yara.

Ban daina bin hanyar shagon Wada saboda wulakanci ko cin zarafin samarin da ke taruwa a wurin ba, sai don girmamawar da ake yi mun din bana sonta sannan a mafi yawancin lokaci bayan sun girmanma min sai kuma in ji su suna fadin wai akan wannan maigida Wada ya bar mu ya tafi, wai dukk kyawawan matan dake garin nan shi babu

wacce ta yi mishi sai ita, abokin maganar in bai danganci Wada ba sai ka ji ya ce, kai itama wannan din mai kyau ce, ai a tsaye take

gata doguwa, ga ta da sura mai kyau, kalan jikinta ma mai kyau ne, haka nan idanuwanta hanci ne kawai ba ta da shi, amma har suman kanta ai mai yawa ne, kuma dubi yanayin tafiyarta ma, kai dai kawai bai yi dabara ba da ya tafi da takaicinta, ai da saku kawai ya yi ku ka sato mishi ita ya samu wani wuri ya rufe ta yana kulawa da komai nata randa ya ji ta ishe shi sai kawai a fito da ita taje ta auri duk wanda taga dama, oho ya riga ya gama mata aiki ina ce shi kenan? A ce eh kuwa to ba zai yarda ba wai yana ganin girmanta alhalin ita din ba ta ga nashi girman ba, don haka na canza hanya.

Iyaka dai sú biyo ni gida su gaishe ni, su fita su yi tafiyarsu. Sujaro dai kullum sai ya zo gidanmu da safe ya yi 'yan share-share in ban yi sauri na yi wanke-wanke ba sai ya yi ko a igiya yaga na wanke kayana na shànya zai kwashe ya je ya goge, haka nan shagon

shayin Wada kullum za su aiko mun da abin karyawa, na yi-na yi su daina sun ki.

Inna ta dawo gida a dalilin ta dan ji sauki,

an dai ce a kiyayi bacin ranta, kuma kar ta rinka zuwa bakin wuta ni dai mu'amallata da ita nesa-nesa ne don wai ina cikin abin da take gani ran nata ya baci.

Na kai wajen watanni uku da haihuwa, Inna bata wani samu lafiya ba, zamana da ita babu dadi, gani cikin kewa bana cikin natsuwata kullum a cikin tunani nake babu halin in ga yaro a hannun uwarshi sai in rinka kwatanta girmanshi da na Abbana tun ma ba in ji su suna sannin juna ba, Wada kuwa danne zuciyata nake yi in rinka gaya mata cewar ba shi ne damuwata ba, bayan kumna kullum na zauna a daki bani da wani tunani sai nashi in rinka tuna kalmominshi ina danganta su da na Kabir Modibbo, ina gwadawa.

Rannan ina kwance a dakina ni kadai tun asuba ake zabga ruwa ba a dauke ba har gari bargo na ke lullube, amma ban daina jin ya waye, har yanzu wajen karfe tara a cikin

sanyin da nake ji ba, tuna ranar da ruwa ya tsare Wada a gidanmu ya shigo dakUna da

nufin wai zai fake ruwan ya zauna ya dan takura kadan ya daga ido ya kalli rufin dakin kafin ya sake dawo da kallon nashi gare ni, ya yi tsaki ya ce "Ke dai ba ki da wayo ko na anini, ki maida kanki bazawara da damunannan? Ga ki kuma da ciki abubuwa biyu da ki ke bukatar kulawar maigida akan su ya rinka tarairayarki kuna jin dumin juna amma kin ki, ni ko ba ni da aure Inna hango damuna ai 'zan nemi wata 'yar bazawara mai dan fasali in ara in kare yawa, don Inna jure wa yanayin zafi to bana iya jurewa yanayi biyu na sanyi da na damuna, gaskiya a wadannan lokutan hakuri na ba mai yawa ba ne, na kalle shi na tabe baki na ce mishi kai kuma abin da ka tasa a gaba ke nan? Ya ce eh, to ni namiji ne mai lafiya, na kalle shi na ce, to ba sai ka nuna marasa latiya ba,. ya ce suna nan ko ba su da yawa dai nasan wani mai lafiya yana barin matanshi na aure ya shekara in dai ba ketare iyaka ake yi a can ba, ai kin a babu lafiya, na bude baki zan yi

magana sai ya yi maza ya ce min, sakarya

kawai wacce bata san ciwon kanta ba, wacce bata san menene rayuwa ba, wacce saboda dakikanci ta kasa bude ido ta fahimci abin da ke kewaye da ita, kulalan idanuwanki basa da wani amfani don basa hange miki komai gara na makaho mai basira da su yana cikin maganar aka yi cida tsawa ta biyo baya na dan razana saboda karfin ta ya yi maza ya karanto wasu addu'o'i yana mai kallon kofar dakin, yan dakiku kadan ruwan ya sake karuwa ya kalle ni ya ce min kin ga ban ga alamar ruwan nan zai dauke yanzu ba, ina bukatar kusantar iyalina in ji dadi na kuma san itama yanzu tana can tana jirana don tasan bana fake ruwa a waje gara ya yi mun duka kan hanyata ta zuwa gida, in naje na same ta sai ta dumama ni, nasan yanzu a shirye take zan je in same ta tana kamshi in kuma ban je ba ma ranta zai baci don na riga na sabar mata da hakan, tunda dai na yi sa'a muna son juna ta kuma juri al'amarina bata gajiya dani, don haka babu wani amfanin zaman da nake yi a nan, yana fadin hakan ya

yi ficewarshi a cikin ruwan ya yi tafiyarshi ya barni ni kadai, babu aure tsakanina da shi amma kishi mai tsanani ne ya murde ni kwana da kwanaki na yi ina fushi dashi babu wanda ya san menene dalili.

Ko a yanzu da nake zaman kadaicin nan Wada mai shayin na tuna na haihu kusan watanni hudu ga shi yau ana-ruwan sama ko inda mun daidai na ce mishi ya bari sai a yau ne aka maida aurenmu me zai faru tsakaninmu? Oho, ina nan a kwance ban ankara ba na ji al'amuran jikina duka sun sauya na yi maza na kankame jikina saboda bana son abin da ke shirin faruwa dani sai dai na kasa hana kaina shiga halin da nake tsoron shigan, gashi na kwanta shiru ina tunanin menene abin yi? Shekara daya da watanni kenan tunda aure na da Wada ya mutu, laifin auren namu ba ni da wata sha'awa mai yawa saboda na fito ne daga gidan Kabir Modibbo, na riga na saba da dabi'unshi ban da haka kuma shi ba mai furta wasu kalamai ba ne da suka danganci mu'amallar mata da miji. Amma auren da na yi da Wada na kwana

biyar da mu'amallar da muka yi a lokacin zaman renon cikin shi da na yi, ya cusa min wata irin dabia saboda halaiyarshi ta furta kalamai a kowane lokaci, ko da kuwa tare da Inna muke ana hira tana kau da jiki zai kawar da wancan zancen ya sako wani yanzu ke zamanki a haka ba ya damunki ko? Ya dan tabe baki ya ce, tausayin ki na ke ji, wancan mutumin katon banza ne, zama da shi ya cuce ki, ya nakasa ki, ya kashe miki zuciya, don ya cire miki sha'awa, ni yaushe zan iya, ai ni ina isa gari in na yi kwana bakwai ina yawo a garin naga ya kwanta min nasan zan iya zama cikinshi in yi wata bakwai to kafin in kafa runfar sana'ata zan fara duba 'yanmatan da ke wuce ni don nasan zan yi aure." Na zubawa Wada ido ina kaHon shi, sai ya yi murmushi ya ce min "ke dai wasa nake yi miki, ke dai ina so in fahimtar da ke ne ni din ina son ki Rahina duk lokacin da na ganki kina zaune haka kuma bana jin dadi sai in ga kamar a takure ki ke in ji tausayin ki ya kama ni, saboda nasan ba kya jin dadi." Yana soma fadin haka zan yi maza in daure fuskata in ce

da tausayin kanka ka rinka ji da ya fi maka, kai da ba za ka iya zama haka kawai ba sai ya tabe baki ya ce, eh to haka ne kuma kina da gaskiya.

Irin wadannan hirarrakin da na saba ji a bakinshi sun lalata ni sun sanya ni a yanzú naa Zamo mai kewar irin zancen nashi, ban iya yin sallar azahar ba rannan sai da na sake yin wanka bayan na safe da na yi saboda in tsarkake Jikina.

Dare yana yi kuwa na maida kofata na rufe na kwanta, saboda kallon da na lura Baba Rahina tana yi min, tun sanda ta ganni da bokiti zan sake yin wanka ina kwance aa dakina na yi sa'a da wuri bacci ya dauke ni ban 6ata lokaci wajen wadansu tunane-tunanen ba sai dai abin takaici baccin inawa bai je ko ina ba, na farka cikin sanyin jiki da kaduwa, saboda mafarkin da na yi na Wadaa mai shayi ba sai na tsaya dogon bayani kan abin da ya faru tsakanina dashi a mafarkin ba, illa iyaka dai in ce maimaitawa ne na abin da ya faru tsakanina dashi a daren amarcin da na yi a gidanshi.

Na shiganga ni Rahina, tawa ta same ni ko kuma in ce na gamu da gamona, ya ya zan yi in fita in yi wanka a gidan nan da asuba ba a ganni ba? Wannan shi ne abin da ya fi damuna, na mika hannu na dauko wayata na duba lokaci, karfe daya da rabi ne na dare, na raya wa zuciyata bari kawai in fita in yi wanka a lokacin koda kuwa da ruwan sanyi ne in dai tsarkake jikina, don kar in samu mas'ala lokacin sallar asuba. A hankali na debi ruwan sanyi a buta a cikin randa na shiga ban dakin kenan na fara wankan ina shisshika saboda kaduwar sanyi sai kawai na ga hasken toclight a kaina, Baba Rahina ce take haska ni, ganina kuma a tuben bai sa ta kawar da hasken touchlight din a kaina ba. "Ai na ce kina bin maza a ka ki kula zancena, to ga shi nan yau na kama ki, wato har cikin gidan dan uwana ki ke kawo mutanen naki? Yana kwance a kabari ba za ki bar shi ya zauna lafiya ba?" Tana fadin haka ta saka kururuwa da iyakacin karfinta, ni kam na yi maza na daura zanina a kirji na wuce ta

don gudun kar Inna ta fito ta ganni a haka.

78

Washegari da sassafe sai ga Yaya Buhari ya iso, na kuma san kiranshi aka yi, ina jin Yaya Buhari yana salati yana karawa, yayin da yake sauraron bayanin da ake yi mishi. Da wani abu ne sabo a ciki ina ce a gidan rawa a ka ce Amirù ya ganta da tsakar dare tun tana budurwa? To balle yanzu da ta san dadin komai, ai ni don dai ina tsoron bacin ran Maude ne kawai ai tun kwanaki na gane ba haka nan kawai ta ke zaune ba."
Inna dai sai faman ku ka take yi, tana fadin ita dai kawai (a roke ni in tafi in bar mata gidan mijinta in yi nesa da ita ba ta son gani na, Yaya Buhari ya ce, to ta ta je ina? bari in je gidan in dawo zan yi magana da matar gidan in yaso ita din sai ta koma can don in sa mata ido kafin ta samu miji a daura mata aure kawai ta tafi tun ba ta sake jawo mana wata magana ba.".
Baba Rahina ta ce, a to, ku ne ai ku ke mantawa da ita, amma ni kawai kullum hankalina da nutsuwata a kanta suke."

nake tunanin ya je neman izini ne wurin
Raihana, shi ya hana shi ta sani a gaba ya ta fi
da ni gidan kamar yanda ya taba yi min a
lokacin da ba ta fi karfin shi ba, na ce kai
Yaya Buhari ma dai shima tashi ta same shi,
ko in ce ya gamu da gamonshi.
Ina cikin zaman tunanin irin damar da
Raihana ta samu a kanshi, ina tambayar kaina
ko me suka yi mishi oho? Sai ga shi ya dawo
tashe da yara a gaba, Baba Rahina ta ce
"Yaya kuma na gan ka da yara haka, dukanku
wijiga-wijiga? Ya ce bari kawai Baba, wai
daga kawai na ce mata Rahina za ta koma can
gidan da zama shi ne ta yi ya ji ta tafi ta bar
min yaran, yanzu zan yi sauri ne in bi ta can
gidan nasu don kar taje ta kulla min sharri."
Baba ta ce, ai gara ka yi sauri ka tafi tunda
dai kai ne mara gaskiya ai tana zaman
zamanta ka je ka tsokane ta wa zai yarda haka
kawai a dauki fitina aje a kai mishi? Da sauri
Yaya Buhari ya fita ya bar gidan ya tafi bikon

matarshi da ta ce ba za ta zauna da ni ba.
A zuciyata na ce, tirkashi, lalle zama bai
same ni ba, tilas in mike in san abin da nake

ciki, tunda dai ko wurin zama bani da shi,
Inna ta ce burinta kawai shi ne in bar mata
gida, gidan Yaya Buharin da nake gadara
dashi matarshi ta yi yaji a kaina, shi kuma ya
tafi bikonta kenan ita ya zaba ba ni ba, na
debi 'yan zannuwana biyu na zuba su a cikin
Jakata na kuma debi kudi masu auki na faki
idon su na yi ficewata na bar musu gidan,
gidan su Surajo na nufa can naje na same shi*
don ba zan iya jiran zuwan nashi ba har ya yi
Sammako ya gama wankin shi shanya yake ta
yi yana ganina ya tare ni cikin murna ya kaini
gaban 1yayenshi muka gaisa sannan muka
sake fitowa waje ina yi mishi tambaya ni
Surajo in saka wani aiki kayi min mana, ya yi
maza ya ce, sa ni mana Anti, ko wane iri ne ai
zan yi miki, na dan kalle shi cikin natsuwa na
dan kawar da kunyar da ke tsakaninmu na ce,
mishi Wada mai shayi na ke so ka tambayo
wurin matarshi ita tunda sun dade tare kuma

yana aurenta ya tafi ina ganin ai ba zata rasa sanin wani abu game da shi ba."
Ya dan kalle ni cikin girmamawa da natsuwa katin ya ce, kamar me kenan? Na ce

ina son sanin gurin shi da kuma sanin shi din wanene? Ya kalle ni ya dan yi murmushi ya ce, ai ina ganin kamar za ki iya finta sanin wadannan al'amuran domin dai shi Mallam aiu mutum ne mai zurfin ciki ne kwarai, in ban da kwanaki uku kafin barin shi kasar nan ai ban san komai game da shi ba, sannan ita wannan mata tashi ni a yanzu ko a hanya na ganta ai sauri nake yi in canza hanyar ba na yarda ta ganni balle har ace kuma in je gabanta da maganarshi, kin san ni Mallam Wada ya aika da takardar sakin aurenta da dukiyar da ya bani in kai mata, wai ta ci abinci da su kafin ta samu wani mijin ta yi aure, a wautata ganin yawan kudin da ya bayar din sai na yi zaton baza ta damu da sakin ba, don haka da na cika umarnin da ya ba ni na cewar kar in kai mata sai na tabbatar ya tafi, yana tafiyar sai na nufi gidan kai

tsaye babu wani damuwa naje na kai mata na kuma yi mata bayanin da ya yi min, tana jin bayanin ta kama wani irin kuka mai tsananin gaske a gabana a firgice na tsuguna gabanta ina ta faman bata hakuri, ban ankara ba kawai

sai na ji hannayenta bisa wuyana ta shake ni da iyakacin karfinta, tana fadin, kai ne Jakadan sakin aure ko? To ai gara kawai in kashe ka don ba ka da wani amfani tunda ba ka iya hada aurcn ba, sai dai kashe shi, da kyar na iya kwatar kaina daga gare ta, na yiwo waje da gudu don haka yanzu ko a hanya ba na yarda mu hadu na kalli Surajo na yi murmushi na ce son shi take yi ne haka? Ya kalle ni ce "Anti kenan." Na ce to ya taba gaya maka kasarsu da garinsu da sunan iyayenshi? Surajo ya gyada kai nuna alamar a'a, sannan ya ci gaba da cewa, na dai san ya aike ni na karbo mishi takardar shiga kasa a Sudan Embasy, ni na yi mishi wannan zirga-zirgan don ya yi amfani da passport ne wanda

ya batar da kamanninshi ya yi shigar mata haka nan ni na taimake shi ya tafi da yaron don..."

Ban saurari don me zai ce ba, na soma yi mishi magana sama-sama, na ce to yanzu ka kyauta/ Yanzu hakan da ka yi wani abin arziki ka yi da har ka ke iya gaya min? Ko ba komai ni da kai ai yan uwa ne, tunda

iyayenmu makwabta ne an haife mu mun taso tare shi ne za ka taimaki bako ya tafi mun da. dana? Dan jaririn da na haifa."

Ya sassauta murya ya ce, To ki yi hakuri Anti, na yi kuskure sai dai ina so in tabbatar miki da cewar zan iya yin kuskuren da ya fi wannan tsanani in da Mallanm Wada zai ba ni umarnin aikata shi."

Na tsaya ina kallon Sirajo cikin zuciyata tunani nake yi yanda a ka yi Wada ya mallaki zuciyar wadannan tsofaffin 'yan iskan yaran suka zamo babu abin da suke so da bin umarninshi kamar shi kuma hakan wai har a bayan i nshi Sirajo sai faman bani hakuri ya

ke yi kan taimakawan da ya yi aka tafi mun da yaro sai dai kuma yana fadin ba wai ya yi nadamar hakan ba ne, tunda umarnin Mallam Wada ya cika.

Ni kam ba tatashi nake yi ba, tunanin al'amarina nake y1, fitowa na yi gida da niyyar tafiya neman jaririna da kuma Wada mai shayi, tunda na gane a gidanmu a yau ba ni da wurin zama, to amma kuma ina zan dosa? Wada ya ce ya baro kasar su a dalilin

Juyin mulkin da bai yi nasara ba a yanzu Sirajo ya gaya min cewar shi ne ya yi mishi takardar shiga kasar Sudan, to yaushe ne a ka yi yunkurin juyin mulki a kasar Sudan?

Wannan ita.ce tambayar da ta zo raina, Sudan ne kasar su ko kuwa zai bata da sawu ne kawai ya shiga Sudan daga can kuma ya nufi wata kasar kuma? Ina kaiwa nan sai na gane shi din Wada irin mutanen nanne masu cewva za su yi gabas su nufi yamma, ko arcwa don haka tafiya nemanshi ba karamin al'amari ba ne, gara in tsaya in kara shiri tukuna, in yi bincike kan kasashenmu na Afrika in ji ta in

da na ji labarin juy in mulki to ta can zan nufa, neman shi ba ta kasar Sudan ba, to yanzu ina zan nufa ke nan ko kuwa gida zan koma in saurari hukuncin karshe da za a zartar min a kan zaman gida ko barin shi? Ban kai ga karshen tunanin ba sai ga wani yaron kuša da gidanmu ya zo wucewa.

"Anti Rahina." Na ce na'am Tanimu yaya dai? Ya ce lafiya Innarku ce dai.... ." Gabana ya yi mummunar faduwa da sauri na ce mishi, ta yi me? Ya ce na ga an kawo mota an

tafi da ita asibiti, wai jikinta ya tashi, da gudu na nufi asibitin da dama ta kwanta na kuwa yi sa'a can din aka kai ta, jinintane ya sake tashi har tana sumå a dalilin tashin hankalin da ta gamu dashi na farat daya, na ce na shiganga ni Rahina, na gamu da gamo na komai dai ni ce sanadinshi, tunda dai na san 6acin ran bai wuce na an ganni ina wankan da aka yi zaton wani abu na yi ba.

Muka koma zaman asibiti don wannan karon nima na ki yarda in rinká zaman gida a

asibitin nake wuni in kwana sai dai in zo gida don in dan yi wani abinda ba a rasa ba, to wai a zaman namu na asibiti Anti Raihana ce a tsaye a gun Inna ita kuma Baba Rahina tana karbar baki masu zuwa gaida Inna, kowanne lokaci ka kalle ta hannunta yana digar maiko saboda duk kwanon da aka kawo sai ta bude shi ta ci abin da ke samunshi, suna hira suna ba da labari yayin dà ni kuma nake gefe babu mai mu'amalla da ni a dalilin wai ni ce sanadin ciwon nata, tun farko ga shi kuma na sake yin dalilin tashin shi.

Shi kuwa Yaya Buhari irin cin zarafin da ya yi mun bai misaltuwa, na yi iyakacin kokarina don in fahimtar da shi ba fa wani abu na yi ba, mafarki na yi. Sai kawai ya kalle ni ya ce min kar ki maida ni dan iska mana, ba a gidan rawa Amiru ya ganki ba ne? Na ce a can ne, ya ce "to ba cikin shege ki ka yi ba sanda aka daura miki wancan auren? Na yi maza na ce mishi, shi nc, ya ce to shi ne yanzu za ki ce min mafarki ki ka yi ki ke wanka? Don kin raina ni za ki maida ni yaro

dan karami? Na kalle shi na ce, "To ban raina ka ba yaya Buhari, ban kuma maida kai yaro dan karami ba, abin da ku ke zaton shi na yi sanda nake yarinya 'yar karama na yi ne? Ai na kawo lokacin yi ne yasa na ke yi? Ina fadin haka yasa hannu ya yanke ni da mari, har sau biyu ban motsa ba ina tsaye ina kallon shi, illa iyaka dai bayan tafiyarshi na yi kuka ba kuma don marin da ya yi min din ne yana sani kukan ba, illa bakin ciki da takaicin wai shi din ba zai iya yarda ni ba balle har ya iya amincewa da abin da zan gaya mishi, shima ya yarda lalacewata ta kai har yanda zan iya

shigo da namijin da bai halatta a gare ni ba har cikin gidan ubana.

Ina zaune ina kallon abin da ke faruwa a asibitin daga Anti Raihana zuwa Baba Rahina dai kula da Inna suke yi suna kuma kula da kansu, don rige-rigen karbar kudi suke yi yayin da yaya Buhari ke ta faman daukan nauyin hidimar gaba daya.

An sallamo Inna mun dawo gida da kwana daya ta zartar mun da hukuncin yin nesa da

ita ba zai yiwo ta yi ta zama dani ina cutar da ita ba, ba ciwon da na yi mata sanadin kamuwa da shi ne mas'ala ba, a'a ina cutar ta ne ta hanyar yin abin da bai dace ba ina zubarwa mijinta da mutuncin da ya rayu a cikin shi na kuma hana shi zaman natsuwa a makwancinshi bayan shi ya rayu ne cikin tsantsa ne, Yaya Buhari bai karbi jawabina ba balle Inna don haka ban tsaya neman kare kaina ba na yi maza na fita na bar gidan tashar mota na nufa, sai dai ban san inda zan nufa ba ko motar Sudan din za ni in tafi? Ban sani ba ina zaune cikin taxi da zai kai ni tashar ina tunanin gidan Kabir Modibbo da

mutanen gidan da yanda naje gidan har sau biyu masu gadin gidan ba su barin na shiga ba bisa cewar wai maigidan shi da iyalinshi duka ba sa nan, ban tsaya na yi doguwar tambaya ba saboda sudin sabbin diba ne ba lokacin zamana a gidan ne suka yi aiki ba sannan ina tsoron kar su tabbatar min da cewar wai Modibbo ya tafi da Lari da

ya'yanshi ne shi yasa ban tsananta tambaya, ba, don kar su gaya min abin da zai dame ni. Na isa tasha na ji ana fadin Sokoto, Katsina, Zamfara, ina za ki Hajiya? Wani can ya taso yana fadin a'a wannan tau ta birnin kebbi za ta zo ki shiga mu tashi ciko na sauran mutum daya, jin haka da kuma sanin da na yi birnin Kebbi tafi su duka nisa har ma nasan tana iyaka sosai da Nijar gashi kuma an ce saura mutum daya, motar ta cika na yi. maza na shige cikinta don kar wani ya zo ya riga ni shiga su tafi su barni a tsaye, nan da nan aka shiga karbar kudin fasinjan tunda ga nan nasan tafiyar ba karama ba ce.
Kan ka ce meye wannan? Sai ga mu muna fita daga tashar ina jin abokan zamana suna

fadin to nan da awa goma dai in tafiyar ta yi kyau zamu isa birnin Kcbbi, maganar suke yi suna kallon agogon hannunsu, yayin da suka ci gaba da tattaunawa tsakaninsu su da suka sán in da muka dosa din ni kam hirar suke yi ina sauraronsu can cikin zuciyata kuwa

murna nake yi ina fadin zan yi nesa da su
Inna da su Yaya Buhari ba za su sake jin
duriya ta ba sai sun yi nema sun gaji nan da
nan na samu kaina da tambayar kaina anya za
su neme ni ma kuwa? Hawaye suka yi nufin
zubowa don tausayin kaina na yi maza na
hana su zubowan saboda kar mutanen da
nake tare da su su gane, mas'ala ce dani don
haka na yi maza na maiya ce na yi zamana
cikin natsuwa ina sauraron hirarkin nasu a
irin maganganun da suke ji ne na fahimci ita
birnin Kcbbi, tana can ne cikin jihohin da
suke arewa maso yamman kasar mu Nigeria.
Tafiya ake yi ana hira har aka ji an gaji da
hirar aka yi shiru, tun ba a saba da juna ba har
aka yi sabo mai karfi, an yi tafiya mai
tsananin nisa tun ana tafiya ana fadin sunayen
garuruwa ina ji wani wuri kuma ina gani a

rubuce tunda ni dama ba sanin hanya na yi ba
har kowa ya gani ya ja linzamin bakinshi ya
tsuke, tun ina kallon kan hanya ina rarraba
idanuwa har na gaji na koma gyangyadi,

bude ido kawai na yi a daidai lokacin da
motarmu ke kokarin tsayawa a cikin wani
daji mai wadansu irin dogayen bishiyoyi da
rakuma suna mika bakunansu suna ci ashe
wai wata mata ce ta ce tana bukatar yin fitsari
aka tsaya mata, kusan duk wani dake cikin
motar sai da ya fita aka barni ina zaune ina
tunani cikin raina yanda za ayi mace ta bude
baki a cikin maza ta ce musu wai a tsaya
mata za ta yi fitsari.
An dawo a ka zazzauna shima direba ya
dawo daga na shi taba ruwan, ya mika jarkar
shi ya ajiye yarufe kan motar shi da ya bude
yasha iska, ya karkade hannunshi da tsunma
ya goge su alamar dai tsabtace da shi sannan
ya gama kintsin ya shiga ya zauna da nufin
tayar da motar don ci gaba da tafiyar tamu,
sai dai kuma hakan bai yiwu ba don juyin
duniya aka yi motar nan ta tashi ta ce bata san

labarin ba, tamfar dai ba a kanta muka iso
wannan dajin ba.
"Ku dan dafa min ita." Cikin sauri maza
suka fito suka kama turi, şuka yi har su ka

gaji ba ta dauka ba, a'a menene haka? Suka fito suka taimaki direba suka yi duk tabe-taben da za su yi bai yiwu ba, can wani daga cikin mutanen da ke taimakon direba ya ce, "kai direba dan miko min ringsperner in kwance nan wurin mu gani." Direban ya ce "Kash! ai ba ni da ita, tawa ta bata ina jin kuma wani ne ya karbi aronta bai dawo min da ita ba, sai dai ko mu tari motocin da ke wucewa kan hanya ko za mu yi dace wani ya tsaya ya bamu aronta."

Nan da nan hargowa ta tashi a tsakaninsu, "yaya za ayi kana tafiya mai nisa irin wannan, amma ba zaka hada komai na gyaran motarka ba? Yanzu wa zai tsaya mana a cikin wannan kungurmin dajin yana bamu aron ringsperner." Wani daga cikin su ya ga hayaniyar ba za ta fisshesu ba ya ce, " Jama'á dare fa in ya yi mana a dajin nan lamarin ba zai yi mana dadi ba, da barin maganar nan

muka yi muka nufi bakin hanya muka kama tare motocin ko zamu yi dace wani ya tsaya

ya taimake mu."

Da sauri suka nufi bakin hanyar kowace mota suka hango sai ka ga suka sa hannu suna fadin wait! wait!! ni dai ina zaune hankalina a kwancé yake cikin zuciyata fadi nake yi ku ne masu sauri tunda ku ke da wurin zuwa, amma ni da ban san inda na dosa ba ai duk lokacin da aka isa daidai ne a wurina, muddin dai lafiya a ka sauka.

Hankalina bai soma tashi ba sai da na ga yamma ta soma yi kar dai fa dare ya yi mana a cikin dajin nan, gaba daya kowa hankalinshi a tashe yake direba kuwa yasha zagi shi da motarshi, har sun gaji tun yana rama musu har ya gaji ya karbi kashedin da aka yi mishi, yaja bakinshi ya yi shiru, don gudun kar a nada mishi ta jakkai.

Ana cikin haka ne wata katuwar mota ta iso gingimari a ka tsaida ita, cikin dace suka tsaya taimako muke so ka yi mana dan uwa SO muke ka taimaka a daure motar nan jikin taka ka fitar mana da ita zuwa gari na gaba

kaga da akwai mata da yara kanana cikin

tafiyar tamu."

Direban gingimari ya ce, "Tó ba matsala, in dai ba wanda rashin igiya zai kawo ba da sauri direban motarmu ya fito da igiya aka daure jikin motocin aka soma jan mu, mutanen cikin mota kuwa suka ce da wa aka hada su ba da shi ba? Wato kai dama kasan motarka akwala ce shi yasa ka ke yawo da igiya a boye don duk inda ta mutu maka a daure ta a ja ka? Ina dalilin da kuna sane da motocinku ba masu kyau ba ne ku ke sanya su a irin wadannan dogayen hanyoyin, kuna wahalar da bayin Allah."

Hankalina bai kara tashi ba sai da na ga har karfe tara da rabi na dare muna kan hanya, muna tafiya hakan ya sani shaidawa abokiyar zamana da muke 'yar magana da ita har ma nake taya ta rike 'ya'yanta cewar ni din bakuwa ce ban taba zuwa birnin, kebbi ba, don ko zan yi dace ta ce min to ai sai muje gidanta mu kwana, in yaso gari in ya waye sai in wuce, tana jin na fadi haka ta sake kallona nan da nan kuma ta tsuke fuska

tana fadin, saukar bako ga wannan zamani?
Wuya ne da shi tunda ko kwanaki ga redio najji labari cewa Limamin wani gari ya sauki bakuwa tat gudu mai da diya nai, na ce haka ne ba a wani dade ba sai ta yi hikima zare 'yarta daga kan cinyata, nima na ce a sauka lafiya, na huta ai ban san kina iya hada su su duka uku a kan ta ki ciyar ke kadai ba shi yasa na taya ki wahalar su.
Wajen sha daya da rabi na dare muka sauka a gari Kcbbi ban san wani ya saurari hirar mu da matar nan ba, sai a lokacin na ji mutumin da ke gefenmu ya ce mun "'yarinya na ji kamar kina ambaton bakunta a tare da ke ko?" Na yi maza na ce mishi, eh, ya ce to in kina iyawa biyo ni muje gidana ki kwana cikin iyalina, na ce mishi to, don kuwa bin shi din na ji kamar ya fi min kwana cikin tasha, kwanciyar hankali.
A gidan nashi matarshi ta karbe ni hannu bibiyu, na kwana tare da ita gari ya waye ta bani abin karyawa da ruwan wanka gidan su dan madaidaici mai kyau ga tsabta na ji kamar dai in ce musu su barni nan kawai in yi

zamana, in rinka taimaka mata da dan wanke-wanke, saboda ba ni da tabbas kan za su yarda da bukatar tawa yasa ban furta mata ba, tunda ga abin da makwabciyata ta cikin mota jiya ta soma gaya min, Liman ya sauki bakuwa a gidanshi ta sace mishi da na sake jinjina al'amarin tare da tunanin bakuwa da bata kyauta ba, tunda ta rasa wurin yin sata sai a gidan Liman.

"Har kin shirya da wuri haka? Ina ki ka dosa?" Matar shi ce ta yi min tambayar, na yi maza na tuna sunayen garuruwan da na ji ana ta ambata a hanya jiya na tuna da guda daya na yi maza na ce mata "ai Kamba za ni." Ta yi maza ta rike baki ta ce "hoda! ai ko dai kina da sauran tafiya." Cikin zuciyata na ce, "ko ina ne kamban? Oho, ina jin ta tana gayawa mijinta in da za ni, ya ce to in fito mu ka yi sallama da ita ya taso ni a gaba ina kalle-kallen garin Kebbi hanyoyinsu da yanayin gine-ginensu da suka bani sha'awa har muka iso tasha, Kamba ne ko Wahra ko Illelan wawure, ko illelan...bai bar shi ya karasa ba ya ce mishi kai raba mu da zance

kanbana, ya ce to biyo ni muka nufi w n
mota mutumin nan ya biya na yi mishi godiya
muka yi sallama ya tafi ya barni nan ina ta
tunani, to Kanba wurin wa na dosa? Me ya
hana in yi zamana kawai a birnin Kebbi yanda
ga shi garin ya ba ni sha'awa?
Da kyar motar nan ta cika sai da maka yi
fiye da awa biyu muna zaune a ciki tukuna
sannan muka samu muka fito daga cikin
tasha, bayan an cika mu irin cikawan da ba
zai kwatantu ba.
Muna tafiya ina sauraron hirar fasinjojin
da muke tare a hakan na fahimci garin
Kamba can yake kan iyaka da kasar Nijar,
zuciyata na ce in ta dauro sai in kara yin gaba
in shiga Nijar kaga na kara yin kusa kenan da
Sudan, na yi maza na tuna ashe nan 1nda na
dosa kara yin nesa da Sudan nake yi tunda na
taba ji ana cewa ana bi ta cikin Nijar ne a tafi
Kotono, Togo, Lome, lokacin ne na gane
wautar da na yi da ban nufi Maiduguri ba,
tunda ta can aka ce Sudan din ta ke, ana
tafiya ina tuna Lari da ya;yana da tsohon

mijina Kabir Modibbo da aka ce wai sun

97

dade da barin kasa, wato Kabir yana iya fita da wata mace suje Turai su zauna tare amma ni ya barni washangare a gidanshi sai in ya kure jaruntaka ya fita dani tafiyar da bata wuce ta sati biyu ba, Kabir dina na tuna yanda Larin take kiranshi nan take na ji kishi ya kama ni randa duk na gamu da Lari ban san abin da zai auku a tsakaninmu ba, watakila dai da zan samu yanda nake so to da yaga ta zan yi gida biyu kowa ya huta.

Ina tunanin zuciyata ina kuma jin hirar masu hira a haka sai na fahimci al'amura biyu farko dai garin yana kusa da babban teku, don haka akwai masunta a cikin shi, haka nan garin yana kusa da wani daji, don haka nan ma da akwai maharba a cikin zuci yata ina ta faman canki-canki in naje ina zan dosa? Na dai yanke wa kaina shawarar duk wanda na fara shiga gidanshi to nan zan zauna tsakanin gidan masunta da na maharba.

Muna sauka a tasha muka firfito bakin hanya ina dan kalle-kallena, ban dai yarda na

nuna kaina cewa ban san ko ina ba saboda hirar da na ji mutanen cikin motar na yi, cewa

harkar yau din nan ai ba ka nuna kanka a wuri ka tonawa kanka asiri ka ce kai bako ne, don haka nima na yi maza na wastsake na maida kaina tamfar 'yar gari na daina dari-darin bakunta ina fitowa bakin titi idona ya hango min wani mutum rataye da baka da kori ga hularshi ta saki a kan shi yana tafiya da gudu na nufi wurinshi sai da na gaishe shi cikin ladabi sannan na ce mishi "gisan sarkin harbi na ke nema." Ya kalle ni ya ce, yo ke kuwa assha gidan Sarkin baka ko gidan sarkin maharba, wanne ki ke bida? Na dan yi tunani katin na ce mishi Sarkin baka nake nema, ya ce to biyo ni don kin same shi ban gane abin da yake nufi ba, sai da muka isa wani gida na ga ya wuce cikin gidan kai tsaye ya ce min biyo ni na b1shi muka shiga na tarar da matarshi da yara biyu sai ya kalle ni ya ce min yarınya ni as sarkin baka, me ki ke bida garc ni?

Kan in ce mishi komai matar shi ta yi mazata

gabatar min da abinci mai matukar dadi,
na ci sai da na koshi nasha ruwa sai daga
baya na gane ba komai yasa na ji dadin

99

naman nan ya yi min daban da wanda na saba
ci ba sai don naman farauta ne, cikin zuciyata
na ce ashe dai naman farauta dadi ne dashi?
Sai da muka gaisa sosai cikin kwanciyar
hankali saboda irin tarbar da suka yi min
tamfar dai sun taba sanina, da aka natsa sai na
ce mishi mahaifiyata ce ta kore ni ga gida
saboda an hada ni da ita, shi yasa na taho nan
zan zauna tare da su zan rinka taya su
hidimar gida, ya kalle ni cikin natsuwa ya ce
mahaifiya ki ke magana ko kuwa dai
mahaifi? Na ce mishi a'a mahaifiya ai ni
mahaifina ya dãde da rasuwa tun ina yarınya
yar karama, ya sake zuba min ido yana
kallona zuwa can sai ya ce min, to gaskiya
dai lamarinki da ban mamaki cikin shi ashe
har itama mahaifiya a kan samu sabani da ita
har ta kai ga kora? Kai ina jin ke dai kam da
shedana cikin sha'aninki, yaushe kike fadin

irin wanga batu sannan ki ce kina zama dani?
Ail bai yiwuwa kin kuwa san darajar uwa? Ai
karo tsakanin kwari da dutse bai yiwu, don
haka maza rufawa kan ki asiri ki koma

rokonta gafara, sannan in kina sake fitowa
Kya fito bayan kin dauko sa'a daga gare ta.
Kwana biyun da suka amince in yi a gidan
su don hutawa kafin in juya kullum nasiha
suke yi min shi da matarshi darajar iyaye
suke gaya min musamman kuma uwa, kin
taba ganin wanda ya yi wasa da ita ya gama
da rayuwa lafiya? Tambayar da ya ke ta yi
min ke nan tunda ba amsa na ke ba shi ba sai
ya bai wa kan nashi amsa, da cewar ina? Ai
bai zuwa ko ina take juya mishi baya don
haka maza koma ki nemo albarkarta kar ki
bata rawar ki da tsalle, in ce mishi to ba don
ina son hakan ba.
Rannan ya sallame ni da tsarabar
busasshen nama mai yawa, ya taso ni a gaba
ya kawo ni tasha ya sa ni a mota mai zuwa
birnin Kebbi, yana ta jaddada min maza
koma gaban mahaifiyarki ki roke ta gafara

kin ji yarinya? In har ta gafarta miki ki dawo
ni zan ba ki wurin zama in kuma yi miki
rikon diya."
Na ce to, na gode sai dai cikin zuciyata
fadi na ke yi to me na yi wa Inna da zan

koma gabanta neman gafara? Ita ta cika
tsanani ne kawai da takura kuma a lokacin da
zata yi ba sai a yanzu da girmanka da komai
ni wani garin kawai zan nufa ba zan koma
wani neman gafara ba, har muka tashi daga
tashar nan mutumin yana jikin motar nan
nasiha yake yi min kan iyaye tare da jaddada
fadin musamman uwa, hankali da ita kin ji1?
Tun ina amsawa har na gaji da jin zancen
nashi na kosa motar ta tashi mu tafi." Tana
tashi ya kama daga mun hannu nima ina daga
mishi har muka yi nisa muka bacewa juna.
Muna tafiya a mota wasu samari guda
biyu suna wata hira mai abin mamaki, na
wata sabuwar mahaukaciya da ta shigo birnin
Kebbi mai hana mutane jin tausayinta kana
nufarta da nufin yi mata alheri zata fara gaya
maka wuce abinka kayi tafiyarka ni din ba

abin tausayi ba ce sai kuma ta soma rattabo maka abin da ta yi.
Gaba daya hankalin mutane ya tafi kan wannan hirar kowa na fadin albarkacin bakinshi kan mahaukaciyar nan har muka isa ba a daina tattaunawar ba.

Mun iso gari zamu yi kwanar shataletalen da zamu isa tasha sai na hango wani abin mamaki, yara ne suka rufarwa wata mata da duka kuma babu wanda ya kula da abin da suke yi, da sauri na ce wa direba a sauke ni a nan, to don me ba ki yi magana tun a baya? yaron motar ya tambaye ni ban tanka mishi ba, ana sauke ni na juya da gudu wurin da na hango wancan abin mamaki, kai! kai! kai! ku bari, ya ya ku ke dukan babba ku ba ku da tarbiya ne, ba ku san na gaba da ku ba? Suka tsaitsaya cikin haki suna kallona alamar sun dade suna dukan nata, suka zuba min ido suna kallona.
"Anti wannan ai in ba ki yi hankali ba kema sai kin taya mu dukanta, in ki ka ji maganarta, ina ce cewa aka yi mu girmama

iyaye musamman uwar da ta haife mu?" Na yi maza na ce musu "Eh." Suka ce "To tsaya ki ji abin da ita take cewa ta yi wa tata uwar." Muka maida hankulanmu gare ta a daidai lokacin da ta gama gyara zama kan wani dutse tana zaman sai na ji ta soma magana kamar haka.

"Wai nan da ake kallonta ita din ba karamar ja'ira ba ce, ba kuma mutunci ne da ita ba, sannan duk wani shakiyanci da aka san mutane suna yi, to ita ma ta yagi rabonta a ciki, ta yi 'yar dariya kafin ta sosa keyarta ta ciro kwarkwata ta kashe da 'yan yatsunta sannan ta ce, aure dai wanda ta yi sanadin shi ta kashe shi ko ta yi nasarar hana daurashi suna da yawa." Yara suka kalle ni suka ce "kin soma jin ta ko? Kin soma jin ta ko? Na yi maza na ce musu kai ku yi min shiru a daidai lokacin da na jiwo ta tana cewa, "Duk wadannan abubuwa da ta lissafo ba su ne suka maida ita haka ba, illa alhakin uwa." Ta yi maza ta rike baki nuna alamar mamaki tana fadin "alhaklin uwa." ta kara jinjina kai

don kara girmama al'amarin ta ce, uhun
Mama bata kwashe da kyau da ita ba ta ji jiki
don sanda ta ce ita din takan nishadu ta nada
mata dukan tsiya saboda sace-sacen da take
yi mata da kuma ta samu sa'a ta wabto wata
dukiya a gidan mijinta ta kawo ta boye mama
ta mata sata mai gaba daya itama sai ta yi
mata hukunci mai gaba daya ta cakota ta faki

idon yan abun uban kannen ubanta da ke
gidan ta tsunbulata cikin wawakekekiyar
rijiyar da ke gidan su tana fadin hakan ta
kwashc da wata irin mahaukaciyar dariya.
Yara kuwa suka taso da gudu suka sake
rufe ta da duka suna fadin "Yar jakar uba,
tsunbula uwar taki a rijiya ki ke wa dariya za
kuwa ki gani, ai ligi-ligi zamu yi miki kafin
mu ja ki kema mu je mu tsunbula ki a wancan
rijiyar ta bayan gari don mu rama mata abin
da ki ka yi mata."
Ganin da na yi tamfar za su kasheta, yasa
na ruga da gudu na kama jawo su ina dago su
daga rufan mata da suka yi su kuwa sai fadi
suke yi, "ai in bata gaj1 ba mu ma ba za mu

gaji ba, sau goma ta ce ta bugi uwarta sau goma za mu rama mata muna ganin rijiya kuma zamu ja ta mu tsunbulata a ciki mu sake ramawa uwartata." Na ja yaran nan a kan matar nan har na ga ji ban yi nasara ba, sai wata dabara ta fado min, na cę musu kai ku bar dukan nan haka ku je kawai ku duba rijiya a nan kusa sai kawai mu ja ta muje mu tsunbulata a ciki kowa ya huta." Suka ce to,

da sauri suka watse suka tafi neman rijiyar da za su tsunbula ta.
Suna tafiya ta taso ta sake zama kan dutsen nan sai kawai ta sake buda baki wai zata sake maimaita wannan bayanın nata, na dago kai na zuba mata ido cikin zuciyuata tambayar kaina nake yi, wannan wacce irinn musiba ce? Idanuwanmu suna haduwa na kife a kasa saboda tsananin razanar da na yi, fuskar Lari na gani a tare da ita, ina kwancen nan a kasa cikin tsananin tsoro da kaduwa waiyo ni Rahina me na ke shirin gani yau? Na dan yi karfin hali na sake bude idanuwana a hankali na sake dora mata su don in

tabbatar Lari ce, ita ce mai wannan haukar, Rafafuwanta sunyi subutu-subutu har suna tsagewa saboda tsananin kumburi, alamar dai kafarta ta tako tazo har garin nan.
Ina daga kwancen sai mui-mui da baki nake yi, wai ina kokarin tunano addu'o'in da zan karanta mata na kasa tuna komai, don dama ni ba ma'abociyar karanta addu'o'in ba ce, maimakon addu'a sai na ji zuciyata tana tuna min mu'amallar Lari da mahaifiyarta da

duk wani wanda ya dangance ta, wanda dai yake nufin mu'amallar ta dashi bin umarni ne to bai kwashe kalau da ita ba, ai kam uwarki bata ji dadinki ba Lari, ina fadin hakan na ji zuciyata ta tambaye ni, to ke fa? Ke ta ki uwar ta ji dadinki? Zumbur na tashi na zauna da naga na kasa baiwa kaina amsar na tuna abin da ya fito dani daga gida da sabanin da ni da kaina na ce wa sarkin baka mun samu ni da ita da tambayar da ya yi min na cewar dama kwai da dutse suna karo ne? Ai ban san lokacin da na kurma ihu ba, sa'a ta kawai mutane ba su juwo ni ba da sun ce mahaukata

biyu ne suka hadu, na mike tsaye cikin sauri da nufin tafiya in bai wa Inna hakuri, cikin gaggawa sai kuma na tuna ashe ba'a garinmu nake ba, lokacin ne na tuna tsananin nisan da ke tsakanina da ita, sai kawai naga tamfar ba zan sake ganinta ba, wani abu zai faru dani, waiyo ni Rahina, waiyo tawa ta same ni na kuma gamu da gamona.

Na sake waiwayawa na kalli Lari bata da wata matsala sai rattaba bayani kawai take yi ko kwata bata yi, tamfar dai haddar kalaman

nata ta yi, har zan bude baki in ce mata, ai komai ya same ki daidai ne Lari, don ke da kanki ba za ki iya tunano abin da ki ka yi ba sai na sake jin ta tana jaddada ba abin da ta yin ne ya fi cutar da ita ba, a'a alhakin uwa ne da sauri na sake fadin na shiga uku, waiyo Inna, Inna ki yafe min abin da na yi miki.

Ina cikin haka sai ga yarannan da suka tafi neman rijiya suna dawowa da gudu alamar dai sun samo rijiyar da suka je neman, na kuma tabbatar suna isowa za su janye Lari su tafi da ita, don sun fi karfina suna da yawa

sarkin yawa kuma ya fi sarkin karfi, don haka na yi maza na mike da gudu naje na kama hannun Lari na ce mata zo mu gudu Lari kashe ki wadancan ja'iran yaran za su yi, bata yi musu ba ta biyo ni, muna gudu yaran nan suna rufa mana baya da kyar na yi sa'a mai motar taksi ya tsaya muka fada cikinshi, ya waiwayo ya kalle ni "shata ne?" Na yi maza na ce mishi "eh, shata ne." Ya tada mota ya hau kan hanya ba ki fadi in da zamu ba, na ce mishi gidan mahaukata ya dan waiwayo ya kalle mu kafin ya sake maida hankalinshi kan

hanya, yana yi yana sauraron maganar Lari, na yi maza na kai hannuna wai zan rufe mata baki, ta yi shiru don kar mai taksi nan ya ce zar sauke mu, ina kai hannun nawa bakin ta ta yi wuf ta kai mun hakoranta za ta cije ni, mai taksi ya yi dariya da ma karya miki dan yatsan ta yi ba dai ke tairnako ba? wannan wa zai taimake ta wanda ke fadin ya yi irin Wadannan abubuwa? Kin san darajar aurc kuwa da alhakin wanda ya yi sanadin raba shi? Ko da yake ban san tsakaninku ba don

naga ba kya tsoronta balle ki ji kyama,
watakila can wurinku daya don mu nan
mahaukatanmu basa irin wannan sambatun
mu nan in suna sambatu ma bai wuce kan
kishiya ba, amma ba uwa mahaifiya ba.
Mun isa gidan mahaukata na tasa Lari a
gaba muna tafiya tana maganganunta babu
fashi, nima kuma ina gaya mata, kinyi min
sanadi iri-iri a rayuwata Lari, nasha zuwa
gidan Kabir Modibbo don daukar fansa a
kanki bana samunki da lafiyarki kalau na
same ki to da ban san iyakar abin da zai auku
ba tsakanina da ke, amma a yau da na same ki

Cikin wannan hali ba zan iya barinki cikin
wannan matsananciyar wahalar ba gara in
kawo ki nan su adanaki tunda nan dai babu
mai dukanki, sai da na gama kgmai nasa
hannu a duk inda ya kamata in sa sannan na
mika musu Lari, na fito na samu mai taksi
yana tsaye bai tafi ba, ashe wai fita kawai na
yi na tafi ban biya shi kudinshi ba, na ce
mishi to muje ka kai ni tasha muna tafiya
yana min mita kuruciyarki a fuska kawai

take, amma zuciyarki ta tsofaffi ce.
Ban kula shi ba, ban kuma karyata shi ba,
har a zuciyartawa don kuwa nasan nauyin da
ta dauka din ba karami ba ne.
Mun isa tasha duk wanda na tambaya
motar Jos sai ya rike baki, ya ce wai ai daga
birnin Kebbi in za ki Jos ai sammako ki ke yi,
sai dai ki koma gida gobe daga yin sallar
asuba ki fito, yana gaya min haka na ji
hawaye sun soma zubowa daga idanuna,
goben ta yi min nisa so nake in sadu da Inna
ko da yake dai ga. wani laifin na kara kan
wanda da can na yi na tafi na bar gida har

tsawon kwana biyar ba a san inda nake ba,
amma ina son zuwa gabanta in roke ta gafara.
Ina nan zaune cikin tasha har wajen karfe
shida na yamma da kyar a ka samu mutun
hudu daga cikin bakwai na ce to muje zan
biya cikon kudin direba ya ce sai ya yi sallar
magriba ya fito daga cikin tasha a ka ce to
kan mu yi sallar sai ga wani fasinjan ya zo
muka zama biyar nima na dan samu saukin
biya.

Muka kamo hanya tafiyar ta yi matukar bani tsoro amma ban ko son jin ana cewa dare ya yi nisa ko za a tsaya? Inna na ke son gani so kawai nake yi in ganni a gabanta ko ma me za a yi min yau gaban Inna kawai na ke son zuwa.

Karfe 'shida daidai na shiga gidanmu a tasha muka yi sallar asuba, kai tsaye dakin Innan na shiga ganin Yaya Buhari a gidan ya fahimtar dani har yanzu ijikin nata babu dadi, naje na durkusa da guiwowina a kasa ina kuka na ce mata Inna ki yafe min dukkan laifuffukan da na yi miki, kuma abin da ki ke zaton ina yi din ban yi ba." Yaya Buhari ya

ce "Ai ke al'amarinki sai ke, an sallame mu mun dawo kin sake tafiya kin daga mata hankali, yanzu ina ki ka fito?" Kan in ce mishi komai sai Baba Rahina ta ce mishi, "kwanan gida mana, ai kai ma kasan inda ta fito, baka ga irin sammakon da ta yi ba?" To ta ishe shi taje ta...kan ta karasa sai na katse ta na ce mata, "A'a Baba, Baba bar ni da irin wadannan maganganun ban san dadin da ki

ke ji ba na sabanin dake tsakanina da mahaifiyata, ban san me na yi miki ba ni dai nasan ko ban taba yi miki alheri ba ni 'yar wanki ce."

Baba Rahina ta kama kuka, wai na yi mata gorin abin da na yi mata, don ba ita ta haife ni ba. Yaya Buhari ya kama bata hakuri yana fadin "Ba zaginki ta yi ba Baba, ba ta da lafazi ne kawai na fadan gaskiyar magana, amma ai gaskiyan ta fada Rahina ai abin a tausaya mata ne, duk wani wanda ya shiga wani hali a wannan lokacin ai bai kai ta ba, dan jaririnta ne fa aka ta fi dashi to duk wani wanda ya ke son shi ko ya ji zafin tafiya dashi ai bayan ta yake gaskiya Inna kiyi

hakuri ki yafe mata ki barta ta zauna lafiya ai ke ki ka kore ta da ta tafiu kuma ki ka shiga damuwa, itama ba lafiya ce da ita ba, don ban taba ganm ta y1 irin wannan ramar ba, yau shekara guda da tafiya da yaron nan har yanzu zancen bai kare ba, a ko ina kuma yake a yau in dai' yana raye to ya tsallake dik wani hatsari tun da a yau ba dan jariri ba ne.

Baba Rahina tana jin haka, ta yi ficewarta tana kuka, wai na mata rashin mutunci yana kare ni, tana fita ya kalle ni ya ce min ina ki ka je Rahina? Kar ki ga kamar na yi Sassauci na gaji ne kawai da zuga Inna da ake yi a kanki, me ki ke nema ki zama? Meye burinki a rayuwa? Me ki ke so.ki maida mu daa gidanmu?" Yana jero wadannan tambayoyin ya zabura ya mike yana fadin "Zan yi maganin ganinki zan nuna miki kyale ki kawai nake yi wai shi nutinshi ya rufe ni da duka, na kalle shi cikin natsuwa na ce mishi "Dama barina kawai ka yi don na riga naga abin da ya fi duka ko zagi amfani shi ne darasi, darasin me ki ka gani? Na kwashe labarr tas na gaya mishi tun daga fitana gida

har zuwa dawowana, jikinshi ya yi matukar yin sanyi sai dai bai ji tausayin Lari ba kamar yanda ni da Inna muka dan ji, ya ce ai ita duniya da ki ke kallonta daga yanda ki ka tafiyar da ita ne itama ta ke tafiyar da ke, in har kin dauke ta da sauki to za ki same ta tafi komai sauki in kuwa ki ka dauke ta da za fi

to ta fi gaba ruwa jima, itama Inna labarin Larin ya tsoratata, cikin sauri ta ce wa Yaya Buhari, ai yaudararta ta rinka yi don ta cuce ta, amma ai halinsu ma ba daya ba ne, na yi maza na ce to Inna ki yafe min abin da na yi miki, ta ce na yafe amma dai yaron nan da ki ka yi sanadin raba ni da shi ne ba zan yafe ba sai randa na ganshi a gabana, gabana ya sake faduwa na ce, To Inna na gode da wanda ki ka yi min din."

A na yin haka sai Yaya Buhari ya ce, "To tashi muje mu dawo da Baba Rahina ke kuma sai muje can gidana mu yi wata magana." Na yi maza na ce mishi gidan "Anti Raihana dai kuma na daina shigar shi tunda ta yi yaji a kan ka ce zan je in zauna da ku ka je ka yiwo bikonta, to na bar mata shi kai dai in ina son

ganinka zan je kofar gidan in yi sallama da kai ka fito tun da dai na, yi sa'a ubana da zai bar duniya ya bar min dan dakin da zan zauna a ciki, ai na gode. Baba Rahina kuwa kaje kai kadai ka dawo da ita, itama na daina shiga gidanta, tunda na je ta ce in tafi wurin

uwata ban koma ba, ba kuma zan koma ba."
Ya kalle ni kawai ya ja uban tsaki ya ce
min, "mahaukaciya kawai, mai gaba da
mutanen da bai dace ta yi ba." Na ce "eh su ai
abin da ya dace suka yi min."
To haka aka yi na dan samu saukin fushin
da Inna ke yi da ni, sai dai kuma mu'amallar
ba mai dadi ba ce, da dai so samu ne to da
Baba Rahina barin gidan nan ta yi ta koma
nata ina ganin kamar da mun fi saurin
sasantawa mu koma mu'amallar mu ni da
uwata, to babu halin in furta wannan
maganar, don haka sai na dauki matakin zan
shiga dakin in gyara in yi duk wani aikace-
aikacen gidan zan kuma shiga in gaishe ta
kowane lokaci tunda gaisuwar ce kawai mai
hada mu.

Ita kuwa Anti Raihana in ta zo gidan
kallonta bana yi balle in gaisheta, cikin
zuciyata kuwa kullum sai na ce ni da ke ne
tunda dai burinki ki raba ni da dan uwana
umarmu daya ubanmu daya, ai kuma shi
kenan na sakaki na kulle ban kuma san ranar

da zan bude ki ba."
Ina zaune a dakina ni da Sirajo da ya zo gaishe ni, hira muke yi sai ya kallc ni ya ce min kai amma Anti ina ganin kamar ba ki da lafiya kin ga irin ramar da ki ka yi kuwa? Ga kuma wasu kurarraji da suka feso miki, sannan kina magana kina wani dan tari kohol-kohol."
Na kalle shi na dan yi murmushin karfin hali na ce mishi, in ban rame ba Sirajo me zan yi? Na kwashe labarina da Ina na gaya mishi da abin da ta fada na cewar wai sai taga yaron a gabanta za ta yafe min."
Ya ce "too! ya gyada kai ya ce kin kuwa san maganar uwa ba karamin abu ba ne, don ko sanda nake shaye-shayena ban yarda na samu matsala da ita ba, to ke ta fadi haka amma shi ne ki ke zaune shiru? Na ce to yaya

zan yi Sirajo? Kwana biyu in bana nan a gida ace yawo najc in ban da haka ai da tuni na dade da nemanshi."
Ya ce, haka ne, to bari mu gani kwana biyu bayan nan Sirajo ya dawo ya ce min ya

yi tunani shi ne ya dace ya tafi neman
Mallam Wada ba ni da kaina ba, ai shi
Mallam Wadan ya ce mishi ya gifmamani in
kuwa yana girmama ni ai ba zan yi wannana
tafiyar shi yana zaune ba, duk kokarin da na
yi na in hana Sirajo yin tafiyar bai hanu ba,
na ce mishi to iyayenka fa? Ya ce na roke su
sun yarda ban kuma gaya musu kina da
hannu a tafiyar tawa ba, saboda kar wani
dalili ya zo su rinka ganinki da abin ke dai
kawai ki kula min da su ki kuma rike min
uwata amana.
Na ce mishi "to Sirajo, na kawo guzuri
mai yawa na bashi, ya yi godiya ya tashi ya
tafi.
Rannan da daddare na yi mummunan
mafarki a kan shi, shi da tafiyar tashi
washegari ina idar da sallar asuba na tashi na
nufi gidan nasu da niyyar in ce mishi ya bar

tafiyar sai kawai Innarshi ce ta ce mun ai tun
hudun asuba ya yi mata sallamna ya tafi wai
zai yi salla r asuba a wani gari.

Cikina ya ba da sautin kulululu, nan takc
na ji babu abin da na ke so irin in zaga
bandaki, da sauri na juya na dawo gida nazo
na zauna, rannan dai na shiga bandaki ya kai
sau goma.
Baba Rahina tun tana shiru don wai ta
daina shiga harkata tunda ta yi magana na
bata amsa har ta ga ji ta ce wannan wacce irin
gudawa ce in ce ko dai ba jamgwam din nan
ki ka je ki ka dangwalo ba ko? Ga kurarraji
ga tari ga rama ga baki ga gudawa, ai shi
kenan alamominshi kenan da kullum a ke
fadi a cikin redio."
Da sauri Inna ta tambaye ta alamomin
me? Ta ce a'a ta ji Maude kamar ba da ita
muke sauraroon redion nan ba, kanjamau
mana, sai da Inna ta timo daga kan gado
saboda tsananin razanar da ta yi, nima na
sake tsugewa da gudawar a dalilin tsananin
firgitar da na yi domin duk abin da ta lissafa
din ina yin su kurarraji dai sun feso min don

ma ba a ganin na wajen sharabata ina rufewa

ga tari kullum hana ni bacci yake yi gashi na ramc na yi baki ga wani abin da ba su san da shi ba kullum wuni nake yi cikin ciwon kai, matsananci.

Da yamma na lallaba na tafi wajen wani kemis din da nake mutunci da mai shi, na ce mishi gwajin jini nake so ya yi min, gwajin na HIV ya ce yauwa to gara dai da ke ki ka yi jarunta ki ka kawo kanki da kanki ai tun kwanaki naso. in ba ki shawarar na fasa kin san maganar ba karama ba ce, domin shi wannan ciwo ba karamin ciwo ba ne, saboda karya garkuwan jiki yake yi, da farkon baiyanarshi kafin a soma samun maganin rage karfin nan na shi ma kin san har kirari ake yi mishi...na yi maza na daka mishi tsawa na ce mishi, bana son ji ka je kawai ka yi min abin da na ce ka yi min, ya ce to Hajiya.

Na dawo gida hankalina ya kara tashi yanzu ya ya zan yi in aka ce kanjamau ne dani? ga shi tun bai tabbata ba ma irin firgitar da Inna ta shiga in ya zamo shi ne ya ya zata

yi kenan? Na yi maza na ce kai ba shi ne da ni ba, to ina ma na je na samo shi? Tunda na rabu da Wada ban hadu da kowa ba, ban je allura ba ba a yi min karin jini ba, wani bai yanke min farce ba to a ina na samu? Cizon da Lari ta yi min ya fado cikin zuciyata, to ai Lari ba kanjamau take yi ba, hauka ne kuma ma ban taba jin an cc ana dauka daga cizo ba, inda haka ne ma ai da masu kanjamau marasa tausayi sun yi ta gantsarawa mutane Cizo da gangan, don haka ba ni da shi kan haka naja na tsaya.

A wannan lokacin Inna ce ina cikin tashin hankali ma bata bakina kawai na yi ga halin da nake ciki ga Innar Sirajo da Sirajo ya tafi ya bar min tafiyar da ya ce tsananin dadewar da zai yi wata uku ne, yanzu ya tasarma wata tara, ba Innar shi ba mace hatta Babanshi rannan a gabäna ya yi kukan rashin dawowar nashi da hawaye, nima na taya su kukan cikin Zuciyata kuwa tambayar kaina nake yi wadannan yan tsofaffi da suka maid ani yarsu suke ta sanya min albarka kan yar hidimar da suke gani ina yi musu inda sun

san ni ne sanadin tafiyar da dansu ya yi wane irin cafta zamu yi? Tausayin su kan kama ni a duk lokacin da na zauna da su suka kama yi min hirar Sirajo irin gagarar da ya yi lokacin kuruciyarshi da yanda ya canza cikin kankanin lokaci ya zama mutumin kirki mai tausayin iyayc, ashe abin ma dan takaitacce ne, suna fadin hakan za ka ga sun kama kuka ni kuma in yi ta basu hakuri, ina fadin ba takaitacce ba ne in Allah ya yarda zai dawvo ba da dadewa ba."

Tafiyar Sirajo ta yi matukar daga min hankali, na kuma yi nadamar barinshi da na yi ya tafi sau cikin kwando, don me ma na gaya mishi damuwata? Don me ni bana iya daukan nauyin al'amarina sai na jefa wani a ciki? Ai muna zaune tare bai taba tunanin bin shi ba, don neman shi sai da na nuna mishi hakan, na yi nadamar tsoma Sirajo da iyayenshi cikin halin da suke ciki na kuma zargi kaina da halin ragwanci da rashin jarumtaka ta yanda na zamo duk wani abin da ya same ni ban rike shi ni kadai sai na tsoma wadansu da ba su ji ba basu gani ba, a ciki

bayan kuma lokacin da na ke shirin jawo abin da ke zamo min damuwar bana daukan shawarar da ake bani.

A wannan lokacin ni da kaina sai na ji na tsani kaina na rinka ganin tamfar ni din daban cc da sauran mutane, na rinka ganin tamfar duk wani ma mutumin da yake nuna mun kulawa ko tausayawa bai sanni ba ne, Baba Rahina da tafi kowa sanina a matsayinta na kanwar ubana ai ga shi nan ta fi kowa kina saboda mugayen halayena da ta sani tuni na daina jin haushin ta na koma tausayin kaina da tunanin yanda za'ayi in gyara mugun halina da ke jawo min abubuwan da suka kewaye ni.

A wannan lokacin da na kara kebe kaina sOsai daga shiga cikin maganar da mutane ke yi ko da kuwa ya ya kusancin mu ya ke da su? Na kan wayi gari bana son zuwa gidan su Surajo don bana son ganin tsofaffin iyayenshi da suka zama abin tausay1, amma sai in ga to in ban je ba yaya zan yi in san halin da suke ciki? Ya ya zan yi in san damuwarsu? Don haka sai in tashi in tafi a hanya in yi ta fata in

je in same su lafiya, don babu abin da na ke tsoro irin in ji daya daga cikinsu yana cewa kin gani ko Rahina, bacci gagara na yake yi gashi kuma wani irin ciwon kirji ya kama ni ba wani dawainiyar asibitin da na ke dauka ne damuwata ba, a'a sai in ga yanda na yi wa tawa uwar sanadin kamuwa da lalura irin ta hawan jini suma zan yi musu, bayan ba su ji ba ba su gani ba, ba ma su ne sanadin zuwana duniyar ba, balle in ce irin tukuicin da na yi musu kenan.

Ina zaune cikin wannan hali ina ji da kaina sai kawai ga Yaya Buhari ya zo da wata maganar da ta fi komai tayar min da hankali, wai zuwa ya yi ya kira ni a gaban Inna da Baba Rahina, yana shaida min cewar shi ya gaji da ganina haka a zaune babu aure, don haka shi din ya shirya kawai zai daura min aure da Amiru tunda dai shi Amirun wai har yanzu yana sona, na yi maza na ce to ni bana son shi mutumin da ya shekara uku sannu ba ta hada ni da shi shi ne zai zo ya ce maka yana sona? Inna ta ce. a iya ai kishi ne da

bakin cikin kin shi da ki ka yi ki ka auri mai

123

Shayin unguwarsu, sai ya dauki abin da ki ka,
yin a matsayin wulakanci."
Na so kwarai a ce cewa Inna na yi to shi
kenan Inna tunda kin fadi haka, ai shi kenan
sai kawai a daura don dai tasan na canza
halin da take cewa in canza, wanda ta ce shi
ne mafi munin halin nawa duka musu da
wanda bai dace in yi musun ba, to amma ina'2
Ni da ke cikin halin kila wa kala na lafiyata,
ni da ke cikin gwaji irin na kanjamau, ga
alamomin shi duk sun baiyana a gare ni, sai
dai kawai wanda bai lura ba, yaya zan yi in
amsa zan auri Amiru? Mutumin da ya dauki
lokaci mai tsawo yana fama da wahalar sona,
ya so ni lokacin budurcina ya so ni bayan na
zama bazawara, har yanzu da na zama abin
tausayi na rame, na fita haiyacina, na yi baki
gaba daya na canza daga yanayina na farko
wai yana sona, to in aure shi a haka? In cuce
shi? shi ne tukuicin da zan yiwa soyaiyar da
ya yi mun? Shi kuma in na shi alhalin ya
tashi kama ni in yi yaya? Anya ba zan fi Lari

lalacewa ba? tunda ita uwarta ta cuta a
tausayi kuwa irin ta uwa ga danta zata iya

yafe mishi a kowane lokaci, to Amiru fa yana
cikin iyalinishi in jona mishi ciwo? Ban san
lokacin da na kalli yaya Buhari na buda baki
na sake ce mishi, kar fa ka fara daura min
aure dashi don na ce maka bana son shi kuma
ban san abin da ya sa ba ka iya zama dani sai
ka shiga harkokina ba, Inna da kanta ta kaiwa
bakina duka saboda jin kalaman nawa, shi
kuwa yaya Buhari sai ce mata ya yi kyalc ta
kawai Inna, ta yi rashin kunyarta ta gama ba
zan fasa daura auren ba, sakarya kawai mara
hankali, da mutunci, ke nan dan tsugunonki
har wani so ki ka sani? zo ki gaya min tunda
ki ke aure wa ki ka taba aura don kina son
shi? Shi dai Kabir Modibbo kin aure shi ne
don ta 6aci auren rufin asiri a ka yi, Wada
kuwa dama auren kisan wuta ne ba don
soyayya ba tunda in da kina son shi da yanzu
kuna nan tare kuna zaman ku tunda ai kowa
ya san bakin cikinki ne ya kore shi daga garin
don haka tunda dama ke ki kan yi aure ne ba

don so ba, sai don wasu dalilai to shima Amirun zan daura miki dashi saboda wasu dalilan, ban sakc cewa komai ba saboda tuni

Zuciyar Inna ta kai matuka wajen baci, ita kuwa Baba Rahina sai tsaki take ta yi, tana fadin tir wannan rashin zuciya ta Amiru ma dai da yawa take, me za ayi da ita?

Bayan fitar Yaya Buhari na bi bayanshi Zuwa gidanshi na je na tsaya a kofar gidan na yi sallama dashi ya fito muka koma gefe muka zauna don ya riga ya saba da haka din, in zo in tsaya daga waje in kira shi ya fito muyi magana in tati ba tare da na shiga gidan shi ba.

Muna Zaman na soma yi m1shi magana a hankali cikin natsuwa ka yi hakuri da rashin kunyar da na yi maka yaya Buhari, ya ce babu komai gaya min kawai abin da ya kawo ki, ai na riga na saba da rashin kunyar taki in har ana sabo na ce to so na ke in gaya maka cewar kar ka daura min aure da Amiru.

Ya yi maza ya ce, wannan ne kuma ba ki

isa ba, ba ke ce gaba dani ba nine gaba da ke ban da ma ce ba ke ce namijin ni mace ba na gaji da duk wani al'amarinki ciki har da abin kunyar da ki ke jawo mana, na saurara ki kawo zawarawa ba ki kawo ba ban kuma taba

ganinki da wanin ba don kin iya wannaan munafurcin babu mai sanin samarinki sai dai a ganki kina wanka in tsofaffin mazanki ki ke jira babu mai dawowa don babu wanda ya ji dadinki ga Kabir Modibbo ma da ki ka yi fafur ki ka ki Wada da dan jariri saboda shi ya ki zuwa sai Amirun dai don haka babu fashi wannan karon zan ba shi ke kowa ya huta.

Na ce mishi in ka bai wa Amiru ni ba ka hutar da shi ba, ka sanya shi ne cikin fitina shi da iyalinshi, ya yi maza ya ce ki je kiyi musu duk abin da za ki iya, na daga ido na kalle shi daidai lokacin da hawaye suka zubo sharrrrr! daga idanuwana, na ce ba zan iya yi mishi komai ba, ina kuma so a yau in tabbatar maka da cewar, Amiru yana cikin mutanen da

nake girmamawa saboda soyaiyar da ya gwada min, ina kuma so in gaya maka na bijire wa auren shi ne a yau ba don kiyaiya ba sai don ba zan iya cutar da shi ba, ko a can baya kuwa ban taba kin Amiru don kiyaiya ba sai don wasu dalilai da suka hana ni auren shi.

Jikin yaya Buhari ya yi sanyi ya zuba mun ido yana kallona cikin natsuwa fushin da ke tarc da shi kuma ya tafi, menene ya faru Rahina? menene damuwarki? Na ce mishi babu komai, na kama kuka sosai don na kasa hana kaina yin kukan.,
Yaya Buhari ya gigice alamar hankalinshi ya tashi da kukan nawa, me ya same ki Rahina? Menene damuwarki? In ba ki gaya min ba kina da wani da zaki je ki gayawa ne? Mu shiga daga ciki, na yi maza na ce mishi a'a ba zan shiga ba gida zani ya ce aa tsaya muyi magana Rahina kar ki tafi ki bar ni cikin duhu kin riga kin tayar min da hankali, kin sanya ni cikin tunani don haka tsaya

kawal muyi magana in san me muke ciki?
Matsawar da Yaya Buharı ya yi yasa na gaya
mishi, me yasa tuntuni ba ki gaya min ba?
Me yasa ki ka kame bakinki ki ka yi shiru?
Na ce saboda Inna nc saboda kar ta ji
hankalinta ya sake tashi yanzu ma kuma ina
rokon mu bar maganar kawai a tsakanina da
kai kar ta kai gare ta don ina tsoron abin da
zai biyo bayan hakan.

Tashi muje wurin mai kemis mu ji inda ya
je aka yi mishi wannan gwajin.
Akan hanyarmu ta zuwa can din na soma
gane ashe dai ni din ma da 'yar jarumtakata,
yawa ne dai kawai bata dashi, sau biyu Yaya
Buhari yana buga tuntuben da ya kusa kifar
dashi a Rasa, dan lambatun da ke kofar
shagon mai kemis kuwa kas atsallake shi ya
yi sai da ya zauna ya shiga cikin shi sannan
ya haura da kyar ya fita.
Zo nan Bala, zo ka gaya min me ka ce
yana damun 'yar uwata? Bala mai kemis ya
matso yana cewa sannu dai Alhaji Buhari,
'yar uwarka ai ta ki yarda ne ta soma shan

magani da bata yi wannan mummunan ramar ba, na gaya mata in ma tana Jin kunya ne da tsoro na kar a ganta a Cikinsu to ni tazo nan zan rinka saida mata maganin a kan farashi mai rahusa, tunda dai gashi nan ko ina kuma wannan al'amari ma fa yanzu nema ya kc ya zama ruwan dare wai gama duniya shi yasa kungiyar lafiya ta duniya WHO tasa hannu cikin al'amarin don a taimaka wa masu fama da shi yanzu in ka kalli cutar koda da hanta

da irin su. Yaya Buhari ya dakatar da shi ya ce, surutu ka ke yi min ba ka bani amsa ba, menenc Ciwon da ka ce yana damunta? Shi kenan abin da na ke son ji.
Bala ya ce, to. shi kenan HIV ne positive shi kenan ko tunda ka ce ba ka son bayanin kwantar da hankali ina kokarin in fahimtar da kai ka gane cewa akwai cututtuka iri-iri da ake fama da su masu tsanani da dan adam ya ke iya rayuwa da su in har zai bi ka'ida."
Yaya Buhari ya nemi kujera ya zauna, gumi ya soma keto mishi tamfar ruwa ake kuza mishi.

Bala mai kemis kuwa sai bayanai yake yi mishi gani yake yi tamfar dai shi din yake sauraro, da dai ya gaji sai ya ce mishi, kai Bala rufe min wannan kazamin bakin naka tun ban yunkura na shakeka ba ina ma aunin naka da ka yimata awon da ya ba ka wannan sakamakon? Bala ya yi zuru yana kallon shi ni ne mai kazamin baki? To na ji kuje ku masu bakuna da tsatta dadin abin dai bani na kar zomon ba rataye kawai a ka bani, shi yasa ba na yarda in yiwa mutane irin wannan

8wajin suje su jangwalowa kansu musiba in ka gaya misu gaskiya su ce da wa aka gama su ba da kai ba? Da duk ana jin kashedin da ake yi ai da ba haka ba, an cc kowa ya tsaya ga iyalinshi miji ya tsaya ga matanshi mata ta tsaya ga mijinta in kuma mutum yaga jarabarshi ta fi karfinshi sai ya leka can wurin haram to ya nemi condom shi condom din nan gashi nan akwai mai araha akwai mai tsada, ya je ya dauko zai nunawa yaya Buhari tare da fadin to kai kanwarka bata ji ba eye.... Y aya Buhari ya takarkare zai cafke shi

aka dai yi sa'a kwalaben maganin shi ya tarwatsa muka wuce muka tafi gidan shi a hanya yana magana tamfar a cikin magagi.
"Ba ki kyauta min ba Rahina, ba ki yi min adalci ba ni da kowa sai ke don me za ki je ki dauko mana irin wannan al'amarin? kin je kin dauko mana abin da ya fi karfinmu Rahina."
Ya Bude baki cikin tsananin damuwa ya ce, "Yau na gamu da gamona, ni Buhari, tawa ta same ni, ina zan shiga da ke Rahina in nemo miki maganin da za ki warke?"

Muka isa kofar gidan shi naja na tsaya na ce mishi "ka yi hakuri da bacin ran da na ja maka Yaya Buhari, ni zan koma gida." da sauri ya kalle ni ya ce min "a'a nan za ki dawo da zama ni ne ya zama min wajibi in kula da ke in dauki nauyi da dawainiyar duk wata lalurarki in ina nan kina can za ki bukaci wani abin bana kusa."
Na ce mishi "a'a yaya Buhari kyale ni kawai in tafi gida tunda dai kasan na riga na yi rantsuwa..kan in gama bayanin ya daka

min tsawa da iyakacin karfinshi, wuce mu shiga ciki kece za ki gaya min yanda za mu yi ko.nine zan gaya miki? kina nufin wannan fitinar da ki ka jangwalo kina da wani mai hakuri da ita ne bayan ni? hawaye suka zubo da gudu daga idanunshi ya yi maza yasa hannayenshi duka biyu yana goge su alamar bai so a gansu tausayinshi ya kara kama ni da na tuna duk wata wahala da kwaramniya da na ke kwasowa a kan shi ta ke karewa, ni kuma bai taba samun yanda ya ke to a kaina ba hakuri kawai ya ke yi dani.

Na shiga gidan na zauna a kan kujera ba tare da na yi sallama ba balle in ce wa mutanen da na tarar a ciki wani abu jiran shigowar yaya Buharin kawai na ke ji. Raihana ta mike tsaye ta bar falon bayan ta galla min uban harara, ta kuma ja wani dan banzan tsaki ban dai kulata ba don bani da lokacinta a yanzu abin da yakc kaina ya fi karfin wannan, ina jiwo ta daga cikin kicin tana aikinta tana fadin aikin banza aikin wofi ni za'a kawowa ashana da barana? to yanzu

kuma wa ya je ya kira mutum ya ce ya zo? ni ko a shigo gidana ko kar a shigo duk uwar uban su daya, tunda dai dubu kamar mutum da duban da suka fi shi za su shigo ai shi kenan.

Tana ta maganganunta, ni kam ina zaune tadin zuci nake yi ina tambayar kaina yanzu nan shi kenan na kamu da wannan ciwon kenan? ko ambaton sunan shi ba na iyawa da bakina saboda tsananin kin shi da na ke yi mishi.

Ina cikin wanuan tunanin sai ga Yaya Buhari ya shigo da saurinshi ke kadaice a

zaune ina Raihana ta ke? ban amsa mishi ba na yi kamar ban san in da take din ba sai na ji ya kama kwala mata kira ta shigo ba tare da ta amsa mishi ba, ya kalle ta cikin natsuwa ya ce mata kinga Rahina ko? sai da ta bata rai ta kara daurc fuska nuna alamar babu wasa sannan ta ce mishi na ganta mencne sabo a ganin nata? ya yi kamar ba mai zati ta gayaa mishi ba ya ce na kira ki ne 1in gaya miki ta dawo nan gidan da zama saboda tana bukatar kulawata a gare ta, na yi miki alkawarin

Zaman nata anan gidan ba zai cutar da ke da komai ba, in kin ga kin gamsu da bayanin da na yi mikin to taimake ni cikin sauri mu gyara mata wancan dakin na kusa da ke, muje in taya ta debo kayanta, in kuma kin ga duk wannan bayanin da na yi miki bai gamnsar da ke yasa kin amince ba to kina iya tafiya gidanku, gabana ya fadi don ba abin da nasa ran ji kenan ba, ita kuwa sai ta gatsina fuska ta murguda baki ta ce, ai gara min gidan namu dama me na ke Ci a gidan naka in ban da hakuri? Da har za a je a sake dauko min wata fitinar a kawo min? Bari in ba ku wuri

kai da ita in kaga dama ka maida ita matarka, na sakc jin wani mummunan faduwar gaba saboda wannan mummunar maganar da ta yi, shi kuwa ko a jikinshi babu alamar bacin rai a tarc da shi, sai ya ce a'a ita kam ai an haramta min ita ba zan taba aurenta ba, amma zan kawo wacce zata iya zama da ita lafiya."
Ta zo ta wuce shi fuu! da goyon ta za ta fita sai na ji ya ce mata a'a to ji mana, ta dawo ta tsaya tana sauraron shi cikin hụci ga zaton

ta wata magana zai yi mata ta ba da hakuri kamar yanda ya saba, sai ta ji ya ce mata, ai ba jeka ka dawo zamu yi ta yi ba, ke kin riga kin ce ba za ki iya zama da 'yar uwata ba, ni kuma na ce zan zauna da ita, in kin je gidanku ai za ki iya zama da na ki lafiya ko? ta sake daure fuska ta ce, ch su za su yi min abin da take yi min ne? Ya yi maza ya ce a'a ina? sauke min yaron ki ajiye shi anan ungowa takardar ki na sake ki je ki can gidan naku ki zauna da 'yan uwanki lafiya, nima ki bar ni da tawa mu zauna lafiya kafin nan ba da dadewa ba in kawo mata mai iya zama lafiya da ita.

Yanda dan da ke bayan Raihana ya kurma ihu saboda saukewar rashin mutunci da ya ii an yi mishi, haka ni da ta muka kurma ihu lokaci daya tanfar hada-baki muka yi a daidai lokacin da muka ji batun sakin auren saboda tsananin kaduwar da muka yi don bamu taba tsammanin jin hakan ba.

Hausawa suka ce wai mu yi gaba mu ba da labari wasa ya yi kyau,
mu sake bin Rahina ta cikin littafi na hudu don mu ji karshen labarin nata.
Shin wasan nata da juyin da zai yi ya yi mata kyau ko kuwa dai kullum kara cakalkalewar yake yi, kamar yanda ta bamu labari.
Mu gamu cikin littafi na hudun tare suka fito.

Na gode.
Hafsat Chindo Sodangi

17/7/1431